NAHUCE!

(Daga Fushina)

1

Littafin

Sumayyah Abdulkadir
takorikabara@gmail.com

SADAUKARWA

Na sadaukar da wannan littafi ga kawata Fati Nahuche, godiya mai dimbin yawa gareki uwar Salma bisa gudummuwar ki yayin rubuta wannan littafi.

GARGADI

BAN YARDA A KARANTA WANNAN LITTAFI A KOWACCE KAFA TA SADARWA BA KO COPYING DINSA A YANAR GIZO KO KARANTAWA A YOUTUBE BA TARE DA IZNINA BA, YIN HAKAN KARYA DOKA NE KUMA ABIN TUHUMA DAGA LAUYANA BARR. SADIQ RUFAI WALI.

TUKUICI NE

Ga duk makaranta littafaina, wadanda na sani da wadanda ban sani ba.

SHIMFIDA

ZAMFARA STATE, NAJERIYA

Yamma lis, a wata ranar Lahadi, wadda tayi daidai da shida ga watan Yuli, ta shekarar alif dari tara da [illegible]'in da tara da misalin karfe biyar na yamma, majalisarsamarin unguwar Kofar Jange ta hadu, ta cika ta batse cikin birnin ZAMFARAN Najeriya. Opposite wannan majalisa ta samari wani gida ne da za'a iya kira ginin masu kudin da, koko a ce 'yan bokon da,

wanda aka yi wa *renovation* daidai da zamani, gida ne mai asali da tsohon tarihi a unguwar ta (Kofar Jange) da yayi fice sakamakon kasancewar mamallakin sa tsohon dan boko kuma dan siyasa da aka dama dashi a gwamnatin Zamfara tun daga *state* har *federal*.

Ita wannan unguwa KOFAR JANGE unguwa ce mai tsohon tarihi wadda ta samar da jiga-jigan 'yan boko da masu fada aji a jihar Zamfara. A dalilin maigidan tsohon dan siyasa ne wanda ya kare rayuwar sa cikin hidimar al'umma. Wadanda suka gudanar da siyasar su ta gaskiya da rikon amana tun duniya na kwance, lokacin mulkin Janar Abdulsalami Abubakar. Duk wani Bazamfare ya kwana ya tashi da sanin tarihin gidan

Alhaji Mustapha Bilyamin Nahuche.

"GIDAN NAHUCHE!"

Shine lakabin da ake kiran wannan gida a garin Zamfara. A saman gidan ma an rubuta hakan cikin rubutu na ruwan gwal. Gida ne mara tarin iyali domin matar aure daya ce tal tayi rayuwa a cikin sa ba tare da kishiya ba; su biyu ne kadai 'ya'yan gidan a wajen marigayi mahaifin su Hon. Mustapha Bilyamin da mahaifiyar su Hajiya Kaltume (Hajiyar Nahuche).

Wannan zama da samarin nan suka yi ba na komai bane na jiran isowar sa ne, shi kadai ran sa dan Nahuche jikan Nahuche.... da suke matukar kauna, ya kuma zame musu *role-model* wato mutum abun koyi a halayya da dabi'a, da kuma

yadda yake gudanar da kafatanin tsarin rayuwar sa, bi ma'ana, shi mutum ne da suka yiwa kyakkyawar shaida ta saukin kai da girmama matasa; ga sukuni Allah ya bashi, ga tarin kuruciya da zuzzurfan ilmi amma babu ashararanci ko kankani a tare da shi. Bai gaji mahaifin sa ba ta fuskar siyasa, amma ya gaje shi ta fuskar ilmin boko, shi kawai dan boko ne mai ci da gumin, biron sa.

Tun safe suke zaune, har zuwa yanzu da rana ta tasamma faduwa, suna da labarin ya shigo Zamfara a safiyar yau yana gidan sa na GRA, kuma duk ranar da ya shigo matasa da masu neman aiki na unguwar su sun warke, shi ba dan siyasa bane (business tycoon) ne mai kishin matasan yankin sa, sannan mai *connections* a birnin Tarayyah,

suna da tabbacin dole zai zo ya gaida mahaifiyar sa Hajiya Kaltume komai dare, ba zai kwana cikin Zamfara ba, ba tare da ya zo ya ganta da tilon Dan sa ba.

Karfe nawa zai zo ne basu sani ba, in kuma zasu kwana dakon zuwan sa bazasu gaji ba, dalilin zaman su kenan a majalisar kofar gidan Hajiya Kaltume Nahuche.

Hira suke irin ta samari masu jini a jika masu burin da babu ranar cika shi; duka burin su dai shine su zama kamar sa a komai; a ilmi, a dabi'a, a halayya, a kasuwanci, a taimakon al'umma, a irin motocin da yake hawa, a irin *simplelife-style* din sa, a farin jini.....a kyawun sura a komai da komai. A cewar su dai, yana daga cikin masu sa'a a rayuwa in ka

dauke *gwaurantakar* sa da bata dada shi da kasa ba.

Abin kamar hadin baki rediyon hannun daya daga cikin su ta soma kwararo muryar sashen Hausa na BBC (British Broadcasting Corporation) cikin shirin su mai taken: "DOMIN MATASA....."

Mai gabatarwa yayi sallama sannan ya ambaci sunan bakon mako, wanda ya sanya samarin baki daya sakin ihu cikin hargagi irin na samari harda masu mikewa suna daga juna. Shiri ne da sukeyi duk karshen sati wato ranar Lahadi domin tattaunawa da *talentedbusiness tycoons* masu jini a jika irin "HABIBU NAHUCHE....". Domin karfafawa matasa wajen neman na kai da neman ilmi.

Mai gabatarwa, AbdulHadi Taheer, wakilin BBC a jihar

Zamfara, ya ce "Assalamu alaykum masu sauraren muryar Hausa ta BBC, a yau muna tafe ne tare da "NAHUCHE", in nace Nahuche ina nufin HABIB, MUSTAPHA BILYAMIN NAHUCHE……. The propriator of NAHUCHE HOTELS & NAHUCHE GROUP OF HOTELS. Barka da zuwa wannan fili Engnr. Nahuche, matasan Zamfara na son sanin takaitaccen tarihin ka?".

Zuzzurfar muryar sa kasaitacciya ta mazan da suka hantse cikin ilmin addini dana zamani ta kwararo sallama da Bazamfariyar *accent* din sa, wadda banbancin ta da sakkwatanci kadan ne…..

"Assalamu alaykum, sunana Habibu Mustapha Nahuche, ni Bazamfare ne gaba da baya, nayi karatun firamare da sakandire

duka a kauyen Nahuche kafin mahaifi na ya dawo birni a dalilin neman ilmi da neman abinci. Bayan kammala karatuna na sakandire na samu scholarship daga (Petroleum Technology Development Fund) da aka fi sani da PTDF zuwa kasar Germany, na karanci 'Hotels Administration' daga jami'ar Cologne, Germany. Nayi digiri na biyu duk a *Cologne* akan fanni guda. Na dawo gida a shekara ta 2000 na fara aiki da babban hotel din Najeriya na wancan lokacin (Nicon Noga) inda na rike manyan mukamai acan, daga baya na fara ginin hotel dina na farko a garin mu wato Zamfara, daga nan ne abubuwa suka mike har aka samar da NAHUCHE GROUP OF HOTELS a manyan jihohi na

wannan kasa tamu mai albarka. Na taba aure, inada yaro".

Abdulhadi Tahier yayi murmushi yace "masu sauraro zasu so su samu karin haske akan kalmar "*na taba aure*" domin kalma ce mai harshen damo, har yanzu da auren ko babu?"

Wani kasaitaccen murmushi ya saki, wani abu ya soki zuciyar sa, a lokacin da *bafullatanar fuskarta* ta gilma masa kamar walkiya, "ta yaya zai mantata da lokutan kwanaki bakwai?" A hankali kuma cikin karayar murya na tasowar wani tsohon miki yace.

"Duk yadda anka fassara ta, daidai ne!".

Abdulhadi Tahier bai ja tambayar da nisa ba don ya fahimci ya gama amsa ta. Sai ya

dauko maqasudin tattaunawar, wanda shine abinda suke so matasa su amfana da shi.

"Ko menene sirrin da ke karkashin nasarori da habakar 'Nahuche Hotels' akan sauran gidajen saukar baki da muke dasu a kasar Najeriya?"

Bai bata lokaci ba ya amsa.

"Excellent Service Delivery!"

"Shin ina ne NAHUCHE? Domin banda Zamfarawa, ba kowa ya san garin 'Nahuche' da ake kiran ka da ita ba, wadda har ta boye asalin sunanka na yanka? A yanzun ana maganar kasarmu Najeriya ne *in general* da babu babban birnin da baka da Hotel, kana da masu kallon ka *as a role-model* suke kuma son jin wasu daga boyayyun sirrikan rayuwar ka".

"Nahuche karamin kauye ne a karamar hukumar Bungudu.

Ainahin garin Nahuche gari ne dadadde, garin ne da mutanen garin hausawa ne. Mutanen garin bakake ne sid.

A wata shekara garin ya hadu da musibar hare-hare daga wasu garuruwan. An addabi garin da yaqi har suka rasa yadda za suyi. Ana cikin wannan halin ha'ulin, sai wani shahararren mayaqi Ya zo daga Katsina, cikin kabilar *Rumawa*. Rumawa kuma ka san fulani ne kyawawan gaske.

Wannan shahararren mayakin tafiya ta biyo da shi ta cikin garin Nahuche, sai *Kekun Nahuche* (sunan ainihin sarautar Nahuche kenan) Ya roki wannan mayakin da ya taimaka masu kan hare-haren da su ke fama da su. Har yayyi mashi alkawarin idan har yacci wannan yaqin to zai bashshi rabin kassar shi da

kuma sarautar *Uban Dawakin Nahuche*.

Aka yi yaqi, kuma aka samu cin nasara, shi kuma Kekun Nahuche bai manta da alkawarin da ya dauka ba, ya ba wannan mutumin sarautar *Uban Dawaki* (saboda ko da yazo a kan Doki yazo) ya kuma bashi rabin kasar shi Nahuche, shi kuma ya koma Katsina ya zo da iyalin shi suka ci gaba da zaman lafiya da mutanen garin, da *Keku* da *Uban Dawaki* sune ainahin sarautun da ke Nahuche kuma kowanne na mulki *individually*.

Har yanzu akwai rabe-rabe akan sunan wannan Bakatsinen amma mafi yawanci sun ce sunan shi Juli (sunan fulani ne). Juli ya sa ‘ya 'yan shi sun yi makaranta, ciki har da kakanninmu, my grandfather

(Bilyamin Nahuche) yana daga cikin dattijan wannan gari".

"Madallah da wannan kyakkyawan bayani na tarihi akan garin Nahuche, a karshe wane sako gare ka ga matasa masu burin zama manyan (business figures) irin ka a Najeriya?

Wannan karon da murmushi ya amsa.

"Su duba *organizational theory of business,* kafin kafa kowanne irin kasuwanci. Gaskiya, rangwame da rikon amana shine sirrin nasarar kasuwanci, kada a raina riba komai kankantarta. A zama kullum cikin tunanin sababbin hanyoyin habaka kasuwanci a zamanance (technological innovation). Abu na karshe shine mai cin muguwar riba, baya taba

nasara a kasuwanci kuma dukiyar sa bata albarka".

Samarin nan banda ihu ba abinda suke yi lokacin da shirin ya kare, muryar shi kadai tsuma samarin Zamfara take yi, kaunar da suke mishi ba 'yar kadan bace. Da a ce shi mai bin ra'ayin wasu ne ba ra'ayin rikau ba, da ya dade da shiga siyasa "……..Allah ya taimaki Nahuche…….Allah ka bar mana Nahuche……." kawai suke ambato cikin hargowa. Daidai lokacin da motar baka wuluk kirar PORSCHE ta sulmiyo ta shigo layin kamar yadda suka yi tsammani. Suke kuma dakon jira.

Dan sardidin matashi da shi. Habibu Nahuche. Yau ma kamar kullum ya fito yana takun nan nasa *majestically,* cikin farin danyen Voyel mara nauyi dan

shafal, dinkin jikin sa (very simple) wanda aka yi shi dan siriri da farin zare, sai da ya baiwa kowannen su hannu daya bayan daya babu gazawa cikin far'a da sakin fuska, sannan ya kawo ihsanin da ya saba yi musu a dunkule yayi musu, addu'a iri-iri Habibu ya sha ta, bai tsaya sosai ba ya wuce kai tsaye zuwa cikin gidan iyayen sa.

Mahaifin Habibu Alhaji Mustapha Bilyamin Nahuche tsohon dan siyasa ne wanda ya rike manyan mukaman siyasa a jihar Zamfara a lokacin rayuwar sa, yayi dan majalisar dattijai mai wakiltar Zamfara ta kudu, yayi sanatan Zamfara ta kudu, yayi shugaban karamar hukumar su wato Bungudu wadda garin Nahuche ke karkashin ta. Ya rasu ya bar matar aure daya da 'ya'ya biyu mace da namiji.

Itace aunty Badiyya Nahuche, wadda ke aure a garin Kaduna, tanada yara hudu, sannan shi Habib, dake binta, daga kansu Allah bai kara baiwa Haj Kaltume haihuwa ba.

Da sallama ya shiga falon Hajiyarsa, tana kishingide akan tumtum, ta kunna rediyo tana sauraron hirar da ake yi da shi. Shigowar sa tayi daidai da karewar shirin. Ta kashe rediyon tana mai shimfida masa karamin *center carpet,* bakin ta dauke da murmushi, fadi take.

"Habibu bazaka bari ka kwanta ka huta zuwa gobe sannan ka shigo ba? Ka taho tun daga Lagos? Ka san dai tunda samarin nan suka ganka ba bari zasu yi ka huta ba".

Murmushi yayi yana zama akan shimfidar data yi masa, idanun sa cike da kewar ta, da

ganin su zaka san akwai shaquwa da kauna ta musamman bayan ta iyaye da Allah ya riga ya assasa, cikin nutsuwa irin tasa ya sunkuya ya gaisheta, sannan yace "bana taba gajiya dasu Hajiyar mu. They are part of me (su rabin jiki na ne), nima shekarun baya ai kamar su din nake; matashi mai buri. Ina Abdallah?"

Hajiya Kaltume ta nisa, sannan ta ce "Badiyya ta tafi dashi Kaduna hutu, amma gobe insha Allah nace a kawo shi don ku gaisa, kafin ka tafi Makurdi din da ka ce zaka wuce daga nan.

Anya Habibu ina amfanin a dinga yamadidi da kai a kafafen yada labarai ana fadin baka da aure sai kace wani dan siyasa? Shin ita ta kara tuna ka a duka wadannan shekarun nan ko bata

san inda kake ba da dan ta? In tana da niyyar cigaba da rayuwa da kai ai da tuni ta nemeka. Tunda na tabbata ta san inda ka ke. Kai ne baka san inda take ba. Kai din a yanzu kuma fitacce ne kuma sananne a kasar Najeriya, bai yuwuwa ace bata san da wanzuwar ka ba koda a kafafen yada labarai ne. Idan har tana da muradin sake rayuwa da kai.

Mata na duniya babu irin wadanda iyayen su basa kawo min, babu 'yar wanda bazaka aura ba Habibu, ka hakura da yarinyar nan..... ka hakura da ita bisa umarni na!".

Hajiya Kaltume bata ankara da cewa hawaye ne ke zuba daga idon sa ba.....sai da ta kai karshen maganar ta. A fili ta furta

"Yaa Salamu sallim!"

Domin al'amarin Habib da uwar dan sa yafi karfin tunanin ta.

A duk lokacin da ta takura masa da zancen aure karshenta kenan, yayi mata hawaye. Don bai da abin cewa. Shin wacece wannan uwar Abdallah haka? Kuma me ta taka da har ta mallake zuciyar namijin duniya irin dan ta Habibu Nahuche???

****

ABUJA, NAJERIYA

(Cikin Gidajen Likitoci na National Hospital

9:30 am).

Ta kashe rediyon a hankali, zuciyar ta na wani irinragaita, tana

daga cikin wadanda suka fara aikawa BBC sakon *appreciation* din su ga wannan shiri na musamman. Abubuwa masu yawa da suka gabata a birnin *Cologne* din Jamani shekaru GOMA a baya na gilma mata. Wannan ita ce kaddarar su, da har gobe ba wanda ya san ta. Kuma kaddarar data hana ta AURE shekaru goma bayan rabuwar su. Kaddarar data maida rayuwar ta duhu didim; farin ciki bai kara gudana a cikin ta ba; "Kaddarar auren kwana bakwai".

Ta dauki hoton karamin kyakkyawan yaron mai kama da ubansa a komai tana kallo, hawaye na sauka akan fararen sumul-sumul din kundukukinta. Ta san yanzu ya girma, watakila aji hudu na firamare. Cikin kowanne hali dai ta san zai kula

da shi. Damuwar ta ba akan kulawar da zai samu bane domin hakika *Habib Nahuche* zai kula da dan sa har fiye da yadda yake kula da *Hotels* din sa. Damuwar ta akan yadda har gobe ta kasa kallon kowanne namiji da idanun sigar aure, kowa ya zo sai ta ga bai kai shi ba, ko farcen kafar sa bai kama ba, koda kuwa ya fi shi komai na rayuwa.

Duk da cewa ta san shi ne kawai a matsayin dalibin jami'ar Cologne ba'a matsayin sa na yanzun ba (mamallakin Nahuche Hotels) amma tana bibiye da duk wani fadi-tashin sa na rayuwa daga ranar da ya yi *kidnapping* Dan su. Dalilin bibiyar ne bata sani ba har yau, tunda ita tace bata son sa. Farin jini kam har bata san irin nata ba, manema ba irin wadanda Allah bai bata ba, kuma burin Dada shine tayi

aure tun kafin Allah ya dau ranta, amma har gobe ta kasa kallon kan sauran maza da gashi sai dan mutanen Nahuche. *The one that took away her pride* na diya mace. Wanda ta tabbatar zuwa yanzu ya manta da ita, a irin shuhurar da Allah yayi masa cikin shekaru goma kacal da rabuwar su.

Bata san hawaye take ba. Sai da ta ji dandanon gishiri a bakin ta. Hawayen da ta tabbatar bazata daina zubar dasu ba har zuwa karshen rayuwar ta. Idan har rayuwa bata koma yadda take a baya ba; *with him by her side.*

"Auren Wucin Gadi". "Auren kwanaki bakwai kacal". Wadanda abubuwan da suka wakana cikin su sun fi tsayin na shekaru bakwai. Wanda ya samar da kaddarar Dan da ke a

tsakani, Dan da silar zuwan sa duniya ne yayi *connecting* komai, ya hada zukata ya kuma raba su cikin kwanaki bakwai. Jami'ar Cologne din Jamus ita ce tushe, mafari, ginshiki na dukkan walagigin rayuwar data samu kanta. *Plus* rashin cikakken gata da ya baibayeta a lokacin.

Shekaru goma a baya, suka soma tariyo kansu a idanun ta, tamkar a majigi.

*****

(FARKON LABARIN)
SHEKARU GOMA A BAYA

Daga cikin bututun maganar cikin jirgin Boeing745 wanda ya tashi guya kasar Jamus a yau daga filin jirgin saman Murtala Mohammed dake Lagos, bututun sadar da sako na gaggawa ya karade kunnen fasinjoji, "jirgi yana cikin hatsari, jirgin mu yana watangaririya, hazo ya lullube sararin samaniya gabadaya, direbobi sun rasa *direction* din su, a sabili da haka muke shawartar a sanya rigar hatsari, don komai na iya faruwa, sannan ta soma bayanin (how to escape a plane crash) cikin gaggawar magana.

Abinda ya gigita fasinjoji, ya firgita mata da yara, masu kuka na yi, masu salati na yi, bata san sanda ta kankame mutumin dake gefenta ba tana rusar kuka.

"Ina da gyatuma, da Allah da ni kadai ta dogara, dama sai da tace min kada in taho karatun nan, don ba lallai mu sake ganawa ba, don Allah don annabi ka taimaka min kada in mutu, in koma wajen Daada".

Za'a iya cewa shikadai ne bai razana a cikin jirgin ba, da ganin yarinyar ta gama tsurewa, kokari yake yasa mata rigar hadari amma ta bi ta cukuikuiye shi gabadaya.

Ta kankameshi kamar ta samu uwar ta. Duk da cikin tashin hankali suke sai da yaji wani iri a cikin jikin sa da ruhin sa. Da karfi ya yakice ta,

"Hey! Relax, are you not a Moslem? Kiyi addu'a, ki cika ni insa miki rigar kubuta daga hadarin jirgi". Ya soma ambaton "innalillahi wainna ilaihi

raji'oun....." a fili har itama ta kama *eventually*.

Cikin ikon Allah ba'a yi minti talatin ba kuma komai ya daidaita. Hazo ya yaye, jirgi ya daidaita akan hanyar shi, ba jimawa suka sauka a birnin Cologne, Germany.

Kunyar abinda ta aikata kuma ta zo ta lullubeta, ta kasa sake hada ido da shi, ta nemi hanya ta sulale abin ta, cikin nasihohin Daada kafin ta taho har da cewa kada ta yarda jikin ta ya rabi na kowanne namiji haramun ne in ba mijin auren ta ba, yau ba raba ba kadai ta kankame namijin da bata san daga inda yake ba, tana tafe tana waige-waigen neman abokan tafiyar ta.

Bafulatanar Adamawa ce kyakkyawar gaske, doguwa sambaleliya, siririya, shekarunta

sha tara da haihuwa, tana cikin dalibai masu hazaka da gwamnatin jihar Adamawa ta zaba tayi *sponsoring* karatun su na likita zuwa kasar Jamus akan likitancin fidar kunne, hanci da wuya (ENT surgeon) wadanda sunyi karanci a Nijeriya, *specialization* din su shi ake kira (Otorhinolaryngology).

Ta tashi ba tare da iyayen ta ba, sun mutu tun tana kankanuwa, a hannun kakarta Daada wadda ta haifi mahaifin ta ta tashi, don haka duk wani wayo irin na yaran da suka tashi gaban iyaye bata da shi, goyon kaka ce ziryan, mai tarin yarinta, wauta da shagwaba, amma a fannin karatu zaqaqura ce. Daada ita tasa ta a makaranta, hazakarta tun tana karama daban ce data sauran tsararrakin ta. Bata san kowa ba

a danginta sai Dada, Dada ce kawar ta, uwar ta uban ta komai nata.

Hazaqarta ce ta sayo mata kauna a gun malamanta, bayan kammala sakandire wadda ta gwamnati ce, tafi kowa cin WAEC da NECO, B2 guda biyar rus, da A1 a biology, physics, chemistry da lissafi, wannan yasa hukumar makarantar ta bada sunanta a gurbin sukolaship na dalibai biyu masu hazaka 'ya'yan marasa karfi da gwamnatin jiha ta basu.

Komai za'a yi musu, sannan za'a dinga basu alawus na cin abinci, har su gama karatunsu a Jamus wanda zai dauke su tsawon shekaru biyar zuwa bakwai har *specialization* din da a ka tura su su yi. A karshen kowacce shekara zasu zo gida su yi hutu su koma.

Ba karamin dauki ba dadi aka yi da Daada ba, kafin ta barta tahowa Germany, sai da shugabar makarantar su ta zo har gida da kanta ta same ta, ta roketa ta kuma kwantar mata da hankali, ta gaya mata yara irin jikanyar ta ba'a wasa da *talent* din su, irin su ake nema don a farfado da harkar kiwon lafiya a Najeriya, sannan karatun da zata yi (Otorhinolaryngology) babu mai irin shi a fadin Najeriya a wancan lokacin, tayi wa jikanyarta addua ta bita da fatan alkhairi ta bar ta taje, ita kuma zata kula da rayuwar ta acan, akwai kanwarta dake aure a kasar.

Sannan ne Daada ta hakura, amma tace abu na halin rai da tsufa, ko a ina ta samu damar yin aure tayi, koda wanene, in dai musulmi ne, babba ko yaro,

in dai zai rike *maraicin* ta, sabida bata da tabbacin zata dawo ta sameta a raye.

Don haka ne da jirgi ya kusa kifar dasu tafi kowa nadamar wannan tahowa, da ta yi hakuri ta yi zamanta bayan Daada, akan gadon bonon ta, da wannan ajali ya dauketa ne a bayan Daada cikin kwanciyar hankali. Don ta san mutum baya tsallake ajalin sa, saidai inda ajalin kowa yake ne daban.

Suna saukowa daga jirgi ta hau raba idanu, abokan tafiyar ta duk sun kama gaban su, taimakon da Allah yayi mata tana da adireshin jami'ar data zo da duk wasu muhimman takardunta a tare da ita.

"RAHINA OMAR! RAHINAH OMAR!! RAHINAH OMAR!!!"

Taji an kira sunan ta daga baya, da sauri ta juya don ganin

mai kwala mata kira haka, nan da nan ta gane shi, shine *agent* wanda aka turo daga Embassy yayi musu jagora a komai har su gama *registration* dinsu. Kuma tana da hoton sa. Sannan *principal* tace shi zai kaita wajen kanwarta Dr. Laura wadda lakcara ce anan Cologne take aure. Gara ta zauna gidan ta madadin zaman (students hall of residence).

Murmushi ya subuce mata, data hango abokan tafiyar ta tare da shi, suka rankaya cikin babbar mota suka wuce cikin gari.

Sunan ya cigaba da wata irin amsa-kuwwa a kwanyar sa, ba tare da sun ankara da shi ba, sabida a lokacin ya basu baya ".....Raheenah Omar.....". Ya ji amsa-kuwwar wannan suna har

cikin bargon sa. Kamar yadda har zuwa yanzu yake jin ta cukuikuiye a jikin sa. Surar ta bazata taba gushewa daga idanun sa ba, domin bai taba ganin kyakkyawar surar data manne a ruhin sa irin tata ba, sannan *innocentlooks* dake cikin fararen idanun ta wani *sign* ne daya makale a zuciyar sa.

****

<u>FIRST ENCOUNTER (HADUWAR FARKO)</u>

The Cologne Public Library" babban dakin karatu ne na jami'ar Cologne wanda yake lamushe dubunnan dalibai komai yawan su, yawanci daliban anan suke assignments din su. kuma idan kazo a matsayi s on dalibi dole ne kayi *r gis r* da Labirare, a matsayin ta na sabuwar daliba

mai yin registration yau ta shigo labirare tunda wuri, bata kai ga tarewa gidan kanwar principal ba ta zauna tare da abokan tafiyarta a (hall of residence) har zuwa sanda zata kammala da *registration*.

Bayan ta kammala abinda ya kawo ta ta juya zata fita, *accidently* ta bugi mutum wanda ya juya baya yake jera littatafan *Encyclopaedia Britannica* a *bookshelves* na *library* din. Littafan hannunsa suka fadi kasa. Da sauri ta sunkuya tana tsince masa, ta mika masa cikin cewa "i'm sorry……." sorry din ta makale a makoshin ta sakamakon ganin makwabcin ta na jirgi. Wanda ta sulalewa. Ga dukkan alamu ma'aikacin *library* din ne. *A very handsome figure* din data zauna mata a rai sati

biyu da suka wuce, ko na kwana daya bata fasa tuna shi ba.

"You?"

Ya fada yana nuna ta da dan yatsa. "..... matsoraciya mai tsoron mutuwa" ya sake fadi cikin harshen hausa. Murmushi ta yi tayi gaba tana fadin "wa ke son ta? Da jirgin nan ya kifa da ni Dada na ma mutuwa zata yi". Dariya yayi ya bi bayan ta har kofar labirare. "Daga wane gari kika zo?" Bata san meyasa ta samu kanta da kantara masa karya ba tace "Benue" kallon mamaki yayi mata don ko kusa bata yi kama da kabilu ba, face zallar fulani, bafullatana cikakkiya, ita kuwa ta fadi hakan ne sabida Dada ta ce mata *never trust a stranger.* Sai yayi tunanin watakila zama ne ko aiki ya kai su zaman Benue din.

Bai cika ta da tambaya ba, suka yi sallama ta wuce ya wuce, amma da ya koma dakin sa na *accomodation* din dalibai sai ya kasa zaune ya kasa tsaye. Ta yi masa karan -tsaye a zuciya a kan dalilin da bai sani ba. A kuma yadda ya lura bata da wayau, wayau na fahimtar abubuwa muhimmai irin wanda ya samu kansa akan ta, bai taba tunanin aure nan kusa ba, amma yau ji yayi in bai mallaki yarinyar nan ba bazai iya rayuwa ba. Ya manta da abinda ya kawo shi karatu ne kuma a yanzu ne ya fara *masters* din sa, ya samu *part time* job da labirare don ya taimaki kansa, kasancewar kudin da PTDF take basu ko kusa baya isar sa sabida tsadar *studentaccomodation*.

A yau da ya sake haduwa da Raheeenah, sai ya tuna cewa ashe shima namiji ne, ashe yana

da bukatar mahadin rayuwa duka shekarun nan biyar da ya kwashe a Jamus, ashe bai taba haduwa da wadda zuciyar sa zata aminta bane, shiyasa bai taba son aure ba, sai akan Rahinah. Wadda ganin shi da ita bai fi a kirga ba. Gabadaya ya rikice ya birkice ya rasa inda zai sa kan sa. Aure kawai yake so yayi kuma ba da kowa ba sai Rahinah Omar.

Yana da Ubangida limamin masallacin musulmai na jami'ar Colgne wanda ke karatun doctorate, mutumin kasar Maghrib ne, shine ya samar masa aikin da yake yi a *library* yanzu, duk da albashin ba mai yawa bane amma bai nemi komai ya rasa ba, har ya bar cikin jami'a ya kama *private* gida karami a wajen makaranta. Rigimar son aure data shige shi

a yanzu harda kuruciya domin kuwa abinda bai sani ba *infatuation* ke damun sa akan Raheenah ba soyayya ba. Kyawun ta ne ya riba ce shi. *He just wants to have her as a spouse at the age of 27* a lokacin da ya kamata ace karatun sa ne a gaban sa ba mace ba. Ga Hajiyar sa ta dade da samar masa mata a kauyen su, Nahuche. Wadda take matukar so, don 'yar kanin baban sa ne. Jira take ya kammala *masters* ya dawo ayi musu aure.

Amma haduwar sa da Raheenah ta rikita shi ta hargitsa shi, gabadaya ya rasa lissafin sa, bai taba tunanin yin zina a rayuwar shi ba duk da cewa ita tafi komai arha a Cologne, amma ji yake kamar zai iya *raping* Raheeenah in bata

yarda ta aure shi ba, laifin da ya san zai iya kai shi ga hukuncin kisa a kasar turai, ji yake in bai yi aure da Rahinah ba a daidai wannan lokacin zai iya rasa ransa, al'amarin da ya kawo shi gaban ubangidansa *at a smart pace* (afujajan) yana neman mafita.

Dr. Sayyed ya dube shi sosai bayan ya gama jin damuwar sa, da yake malamin Psychology ne a take ya gama fahimtar halin da Habib yake ciki (infatuation/lust), yace masa "ita yarinyar tana son ka, kuma ta amince zata aure ka? Annabi SAW yayi umarni da ayi wa samari aure a lokacin da suka bukaci hakan, in ba haka ba barna bazata gushe ba a doron kasa. Don haka in ta amince ni zan daura muku aure (ba tareda

tunanin abinda zai biyo baya ba)".

Cikin rauni Habib yace "ni ko dosarta da zancen bazan iya ba, i'm sure ba abinda ya kawo ta kenan ba, she's very naive and innocent, ni kuma zan iya cutar da ita idan ta ki yarda ta aure ni, i just want to marry her..... or rape her.....in ba haka ba Dr mutuwa zan yi. Na yarda bayan dayan wannan in kare *behind bars!*".

Dr. Sayed ya gama gane inda Habib ke fuskanta, *infatuation* ne mai tsanani ya kama shi ba soyayya ba, yace "ba zaka mutu ba insha Allahu, kuma bazaka aikata zina ba har karshen rayuwar ka, sannan bazaka je kurkuku akan laifin fyade ba, kaje ka gwada sa'ar ka, in har ta amince ni kuma zan yi

kasadar daura muku aure, ai karatu baya hana aure".

Tun daga lokacin yake tunanin ta inda zai bullo mata, sun sha haduwa a wurare daban daban musamman labirare data ke yawan zuwa. Amma kwarjininta ya hana ya tunkare ta. *Until that fateful day*.....da ya ga an daukota ranga-ranga a sume an yi asibitin jami'ar Cologne da ita a ambulance.

Abokan karatun ta sun tabbatar wa da likita cewa basu san me aka gaya mata a waya ba, ana cikin lecture ta ansa waya sai gani su kayi ta zuba kara ta zube a wurin a sume.

Ya makale a asibitin nan a kofar dakin da aka shiga da ita, ya ki matsawa ko nan da can, lokacin da likitoci suka yi nasarar dawo da numfashin ta shi suka ce ya zauna tare da ita

kasancewar duk abokan karatun ta sun koma makaranta. Sun dauka shima *coursemate* din ta ne.

Tana bude ido da sunan DADA ta bude baki.....tana kuka tana fulatanci, fulatancin da bai san me take fadi ba, a karshe ya tsinci kalmar hausa. ... Dada ni da ke shike nan? Dada kema kin tafi kin bar ni ba uwa ba uba a kasar da bani da kowa? Dada kin kyauta min kenan? Meyasa baki ce mutuwar ta dauke mu tare ba? Me yasa baki jira na zama *Otorhinolaryngologist* ba na saya miki gida mai kyau da mota?"

Ta soma zabura tana fizge karin ruwan ta, da sauri ya rike ta ya kuma danna kararrawar kiran likitoci suka zo suka zurmuqa mata allurar barci.

Kwana uku cif Rahina na cikin wannan halin na tsananin

firgita da dimuwar rasa Kakarta. Ko na minti daya Habib bai bar asibitin nan ba, da nasiha da banbaki da janyo ayoyin Al'qurani masu tabbatar da kowanne mai rai mamaci ne "kullu nafsin za'iqatul maut" Habib ya samu ta soma dawowa hayyacin ta. A ranar data kwana biyar a gadon asibiti, cikin dare ta farka yana sallah, ta hada kai da gwiwa tayi kukan ta ta koshi, yana jin ta har ya gama nafilfilin sa ya juyo don ya kara bata baki.

Sai gani yayi ta mike, ta dauki mayafin ta ta yafa, tana shirin barin dakin. Yayi maza ya sha gaban ta "Rahina ina zuwa? Likita bai sallame ki ba tukunna, ya ce sai gobe, kiyi hakuri ki kwanta ki kara nutsuwa zuwa gobe, ni da kaina zan maida ke gidan ku".

Cikin kuka ta ce "Najeriya zan koma na fasa karatun, *passport* dina zan je in dauko a gidan aunty Laura, dama sun tsane ni, a dole nake zaune a gidan, bazan iya rayuwa babu Daada ba, don Allah.....don Allah ka fadawa hukumar makaranta na koma gida".

Wani matsanacin tausayin ta ne ya kama shi, yace "Rahinah in kin bar karatun ki, kuma babu Dada, kin koma gida, menene madafarki a gaba? Gara ki karbi *reality* na cewa Dada ta rasu, ki tsaya ki gina *future* din ki, wanda ya riga ya mutu baya dawowa, kiyi hakuri zuwa gobe likita ya sallameki in raka ki gidan Antin ki, in kuma san gidan naku don yanzu ni Yayanki ne wanda bazai bari ki ragaita a rayuwa ba".

Da haka ya samu ya kalallameta, da tausasan lafuza, har ta yarda ta koma gado ta zauna. Saidai yadda suka ga rana haka suka ga dare. Kowanne abinda yake sakawa a ransa daban ne. Ga Habibu, tunani yake wannan dama ce Allah ya bashi ta auren Rahinah cikin sauki, tunda bata da gatan da zai zame masa cikas, ba sai ya wahalar da kansa wajen neman soyayyar ta ba.

Raheenah kuwa tunanin ta irin zaman data fuskanta ana yi a gidan anty Laura ne; zama na kafirci da rashin tuna dokokin ubangiji, ta tsani zaman gidan don dai bata da yadda zata yi ne, sabida basu da kirki ko kadan, Anty Laura tana da wani Da Yasir fitinanne mai ruwan 'yan iska, wanda ta gama gane take-takensa na banza da wofi a

kanta, don haka tunda ta yi sati a gidan ta fahimci zaman gidan bazai yiwu mata ba domin 'ya'yan anty Laura ko sallah basa yi. Yanzu tunanin ta shine taje ta kwashe kayanta ta dauki *passport* din ta ta koma makaranta da zama yadda ta fara tun farko. Tunda Habib ya ce komawar ta gida ba amfani.

Gari na wayewa likita ya sallame su, suka fito tare zuwa bakin titi, ya tare musu taxi suka hau zuwa gidan Dr. Laura wanda ba shi da nisa da makarantar su.

Cikin halin ko'in 'kula Dr. Laura ke tambayar ta inda ta tafi har kwana biyar, bayan an gaya mata kakarta ta rasu, shi kuma wannan saurayin ina ta samo shi?" Kamala da kwarjinin Habib yasa ta kasa ci masa mutunci yadda tayi niyya, a take ya kara

fahimtar cewa dan sauran gatan da yake tunanin tana dashi a kasar ma babu, wannan matar da gani ba jinin ta bace ba.

Nan yayi mata bayanin daga asibiti suke, ya gaya mata duk halin da Rahina ta kasance, ga mamakin sa sai ta kyabe baki, "don tsohuwa ta mutu ne kike neman kashe kanki? Ai kawai yarinya ki zauna kiyi rayuwa mai 'yanci a Jamus ki tarawa kanki ilmi da dukiya, kin ganni nan tun da na bar Africa na huta da wahala, aure kuwa na yi ya kai goma, yarannan da kike gani duk uban su daban, bana daukar bakin cikin namiji, in kika samu kwalin Cologne kin gama tsallakewa, ki tsaya kiyi karatu ki nemi rayuwar 'yanci kawai".

Rahina ta saki baki tana kallon ta, Shikuma Habib tsoron matar ne ya kama shi, ya tabbata

barin ta da Rahinah hatsari ne babba, don haka ya yi gaggawar cewa shi yana son auren Rahina, a bashi auren ta.

Aunty Laura tace "ai ba 'ya ta bace, ba kuma 'yar uwata bace, student din yayata ce kawai, don haka zan mata magana, in ta amince kuma kanada sana'ar da zaka rike ta ko gobe zan wakilta muji na ya daura muku aure".

Abu kamar wasa karamar magana ta zama babba, domin principal cewa tayi Dada ta bar mata wasiyyar idan Rahina ta samu miji musulmi, wanda zai rike maraicin ta ayi mata aure shine babban kwanciyar hankalin ta a kabarin ta.

Dr. Laura tace "ai gashi kam ta samu, har da tabon sallah a goshin sa karewa, kuma ga yadda na lura yana son ta sosai,

zan gaya wa baban Nihal ya zama waliyyinta ranar jumaa a daura musu aure".

Baban Nihal mijin Anty Laura da Dr. Sayed suka zaunar da Raheena suna nuna mata amfanin tayi aure shine martaba da kwanciyar hankalin ta, Rahina ta kasa musa musu sai kuka, daga Sayed ya dinga lallashin ta, daga bisani suka daura auren a masallacin Cologne bayan an idar da sallahr jumaah, akan sadakin da Dr. Sayed ya biya masa *in Euros*. Kudi tsababa masu yawa duk don ya taimaka ta amshi auren domin ta kafe kai da fata bayan daurin auren tace bata so, duk da *convincing* din ta da Dr. Sayed ya bata lokaci yayi, har mari ta sha a wajen anty Laura tace "ubanki ya ce ki kwaso min shi? Ba tare na gan ku ba? To in

baki son shi sai dai ki bar min gida na, ko ki auri Yasir ya sha *cocaine* dinsa ya lakadaki ba ruwa na".

Ta debi kudin sadakin ta watsa mata, tace "kije ki hada kayan ki da daddare zasu zo su tafi dake, Allah ya gani ni taimakon ki na yi, don nasan in bakiyi auren bama karshenta ki zama international prostitute. A Jamus kike yarinya ba a Najeriya ba".

Tana kuka tana komai Anty Laura dasu Nihal suka loda mata kayan ta a bayan taxi din da Habib ya zo a ciki, kamar dama zaman ta tare dasu ya takura musu don dai basu da yadda zasu yi da ita ne.

Tunda suka shigo motar take kuka, kuka tukuru tamkar zata fidda rayuwarta. Wannan wace irin rayuwa ce? Daga ganin

mutum bata san komai a kan shi ba, don kawai musulmi ne kuma ya zo daga kasarta sai a aura mata? Kawai don an ga bata da gata? Ita bata ce lallai sai ta zauna da Dr. Laura ba ta so ta koma hostel kawai tunda ko ta koma Najeriya babu Dada wajen wa zata je?

Tunda ta taso bata san kowa nata ba sai Dada, daga dangin uwa har na uba, ta rayu karkashin kulawar tsohuwa Dada a shekarun rayuwarta bakidaya. Yau ga rayuwar da rashin gatan Dada ya jefa ta a ciki; auren mutumin da bata sani ba, bata san asalin sa ba, bata san halayen sa ba, bata san manufar sa a kanta ba. *Just* haduwar kan hanya wadda bazata iya bada shaidar komai a kan sa ba, wannan taimako nasa ya zame mata masifa, duk yadda

aka yi yana da *target* dinsa a kanta, amma in ba haka ba ta yaya daga ganin ta bai san asalin ta ba zai zabe ta ta zama matar auren sa?

Ko da take goyon kaka, tana da hankalin ta. Bazata taba barin shi ya gurbata mata rayuwa ba.

Ta soma yi mishi kallon mutumin kirki tun daga haduwar su ta farko, amma ashe ba haka bane yana da *mission* dinsa da yake son cikawa a kanta.

Zata bashi mamaki, zata nuna mishi ka bar raina allura....karfe ce, komai kankantar ta.

Wannan take hakkin dan adam ne, a aure shi babu cikakkiyar yarda da amincewar sa.

Tana da damar da zata kai su ga hukuma daga su har anty Laura, amma bazata yi hakan ba, sabida ko yaya dukkan su sun taimaketa a Jamus. Kuma Dr. Sayed yayi iya kokarin sa wajen *convincing* din ta.

Amma ta gama kudurta mafita, mafitar da zata nemawa kanta ta kwatarwa kanta 'yanci.....

"*Bazata taba bari ya samu access din keta mata haddi ba, in ma kwadayin hakan ne yasa shi auren ta da gaggawa haka. Har sai ya gaji ya bata 'yancin ta na dalibtaka wanda shine abinda ya kawo ta Jamus ba auren sa ba*".

*****

Kugin karshe da motar tayi, a kofar flat din Habibu ne, wanda ke shiyyar *Klettenberg*.

Shi ya bude mata kofa da kansa ya kuma rungumota barin jikin sa. Ji tayi kamar ya dala mata wuta, amma haka ta daure ta cije ta shiga gidan tana hawaye.

Dr. Sayed ya biyo bayansu har falon gidan, ya zauna yayi musu nasiha sosai, yace su taru su rufawa juna asiri su zauna lafiya, duk wata matsala da suke da ita su sameshi, shi uba ne a garesu, kuma Raheenah ta kwantar da hankalin ta Habib mai son ta ne, bai aureta da wata manufa ba sai bisa son cika sunnar Ma'aiki SAW.

Da wannan yayi musu doguwar addua'a sannan ya tafi, bayan Habib ya taka masa ya rufe gidan ya dawo.

A inda ya barta anan ya sameta, amma ta yaye lullubin fuskarta tana yi masa wani irin kallo, kallo irin na kamar ka ga

makiyin ka, koko abunda zai cutar da kai. Da gaske zuciyar ta da dan kankanin tunanin ta basu bashi kowanne matsayi ba, face na mai mugun nufi a kanta.

Ya zauna dab da ita, har tana iya jin kamshin turarensa Carolina Herrera (Men). Da sauri ta matsa ta ja baya, sannan ta nuna shi da dan yatsa ta soma magana cikin hawaye.

"Allah ya fi ka! Duk abinda kake nufi da ni Allah ya fi ka".

Cikin madaukakin mamaki yake kallon ta, baki sake, ya ce "Rahinah are you alright?""A'a a haukace nake, kawai daga ganin mace akan hanya baka san ko wcece ba sai kasa power ka aureta? Sabida ka fahimci bani da gata ko? Shiyasa ban cancanci ka nemi soyayyata ba, ka nemi dangi na ka aure ni cikin mutunci, ka taimaka min

inyi abinda ya kawo ni sai kawai kayi min kutse a rayuwa ka raba ni da burika na?

Ni na ce maka na zo Jamus don in yi aure ne?"

Habib yayi mata wani irin kallo, domin ji yayi ya muzanta a gaban ta, yarinya tamkar mai gani har hanji! Da gaske yasa kaimi ya aureta ne don biyan bukatar ruhin sa da gangar jikin sa, bai taba fadawa a wani abu wai soyayya ba, kallon ta yake da jin ta *as waste of time,* burin sa da lokutansa na tunanin maida kobo ya koma dari ne, yana da manyan burika da suka zarce *soyayya*. In fact, bai dauki mace a bakin komai ba banda abar hutawar gangar jikin mijin auren ta.

Amma ita wannan inda bata bullo masa ta haka ba, da bata nuna ta san ba son ta yake ba,

bayan *target* dinsa na auren ta yanada burin tallafar rayuwar ta da maraicin ta, tare da cigaba da zama da ita har karshen rayuwar sa.

Amma tunda ta nan ta bullo, ya san ta yadda zai yi maganin ta.

Daga sanda ya mike ya durfafe ta, da sanda ta soma ja da baya cikin tsoro, cikin abinda bai gaza sakan bane idanuwan su suka hadu, ta hango wani boyayyen al'amari cikin *brown* kwayan idanun sa, al'amarin da har gobe ta kasa mantawa, shekaru bakwai kenan; Babu soyayya a cikin a cikin kwayar idon Habibu ko kankani face *lustfuldesire* wanda ya kara darsa mata tsanar sa. Ta kuma kara yarda da cewa manufarsa kenan ta auren ta.

Da farko yayi kokarin lallashin ta, amma sai ya gane zai bata lokacin sa ne kawai, ga rashin kunya da tsiwa kala-kala na fita nau'i-nau'i daga bakin ta, sai ya ce "Raheenah bari in yi maganin ki.....".

Duk wani kokari na kwatar kai da neman ceto Raheenah Omar ta yi, kafin ta gane all her effort was futile (kokarin ta na banza ne), tamkar Habib Nahuche ya jima yana jiran wannan ranar, ya gama shirya mata. Abubuwanda suka wakana a tsayin daren bakidayan sa ba masu dadin fada bane. Saboda al'amarin baida maraba da *rape* banda igiyar aure data suturta shi.

Kuma wannan ne abinda ya gina matsanancin tsoro da kiyayyar sa a zuciyar ta. *She hates him with passion from*

their first night. **Ta alkawartawa ranta koda jan ciki sai ta bar Jamus, gara ta dawo Adamawa ko bara ce ta yi ta ci da kanta, da dai ta zauna da wannan mugun mutumin mai halin dabbobi.**

Tamkar ya san tunanin ta, washegari da zai fita makaranta saida ya kulle ta ta waje.

*****

Ba shi ya dawo ba sai yamma lis, tunda ya san ya bar mata komai da zata bukata. Amma ga mamakin sa a inda ya fita ya barta anan ya dawo ya sameta, a kwance akan marbles kamar kayan wanki, baya tunanin ko sallah ta tashi ta yi, balle akai ga wanka.

"And your name is bride?"

Ya tambayeta cikin zolaya.

Hararar data ke masa tamkar idanunta zasu fado,

wadanda suka kada suka yi jajazur kamar an gumbuda musu barkono. Da za'a bata dama zata iya kashe shi ta hanyar rataya, sabida tsanar data yi masa.

Ya tsugunna a gabanta ya ajiye mata ledar abincin McDonalds da lemun power horse mai sanyi, yana wani makalallen murmushi na tura haushi yace "ki ci ki sha, ko kya wartsake kinji amarya ta! We're going for the second phase.,.... what is the marriage meant for? I don't believe in what is called love. Ban sani ba ko in kika haifa min 'ya'ya..... ""ta Allah ba taka ba..kada Allah ya nuna min wannan ranar""ko?" Ya tambaya yana kara hade filin dake tsakanin su..... kuma wannan karon ma kokarin ta da bijirewar ta, bai kwace ta da komai ba.

"You goddam lunatic! I hate you.....kuma insha Allahu sai Allah ya saka mini, ta hanyar da baka taba zato ba. Abinda kayimin sai an wa 'yar ka, in baka haifa ba kanwar ka, in baka da ita UWARKA!"

Bai san sanda ya daga hannu ya zabga mata mari ba, marin da Raheenah ta tabbatar taga wuta a cikin sa. Kafin ya kama hannun ya rike cikin nadama! Wai shine da dukan mace.....macen ma mai amsa sunan matar sa. Amma abu na karshe da bazai iya dauka ba shine raini, don abinda take gani a matsayin babban laifi daga gare shi shi ko kusa bai kalle shi hakan ba. A tunanin sa ana aure ne for sex only, kamar yadda ake cin abinci kullum. Baya jin a duniya zai so wata mace bayan mahaifiyar sa. Kuma baya

comparing din ta da sauran mata. Talkless of Rahinah ta ambace ta ta zaga.

"Duk rainin ki ya tsaya a tsakanin ni da ke, kada ki sake ki hada da uwata".

Ya fada yana sake rugumota jikin sa ba tareda tausayi ba ya sake maimaita laifinsa, har da cewa "ai sadaki na biya, ki jawomin ayar da tayi umarni da soyayya, aure Ubangiji yayi umarni mu yi ba soyayya ba".

This man is unbelievable ga tunanin Raheenah bata san a rukunin mutanen da zata sanya shi ba, gashi dan boko mai matakin master, amma jakancin sa akan diya mace ko gardin kauye bazai yi ba. *She hates him again and again for his wickedness.* Tunanin ta gabadaya ya koma kan *how to*

escape from this abusive marriage.

Amma har kwanaki suka nausa zuwa biyar, bata samu wannan damar ba.

Yayin da Habib ya dukufa ga morar sadakin sa, don bai taba tunanin abinda yake yi din ba daidai bane, ko zata iya tafiya ta barshi tunda bata da kowa.

(Akwai maza da yawa irin Habibu Nahuche, wadanda baza'a ce rashin ilmi ya hana su son matan su ba, ko kasancewa masu nuna soyayya da tarairaya koda *fake* ce. Suna aure ne for their own pleasure. Ita mace kuwa 'yar son lallashi ce da soyayya kuma har abada in baka iya tafiyar da ita ba, hankalin ta bazai taba nutsuwa da kai ba. Ita Rahinatu ma kallon Habibu take *as rapist* don bata yarda miji zai

iya yiwa matar sa izayar da yake yi mata ba).

A duka kwanakin nan bata ci bata sha, sai taji hanjin cikin ta na neman tsinkewa ne take shan ruwan bunu ko ta sha madarar kwali, wanka kuwa rabon ta dashi har ta manta, watakila in yaji tana tsami, a yadda yake dan gayun nan mai son wanka da kamshi zai daina rabar ta.

Amma gogan nata ko a jikin sa, wani sabon abu ma ya tsiro da shi; fesa mata turaren sa 'Carolina Herrera' a duk sanda zai kusance ta, tana kuka tana tsine masa, amman kaman tana kara zuga shi.

Tsahon kwanaki shida ya tabbatar shi kansa ya samu lafiya daga masifar dake damun shi akan Raheenah, zamu iya cewa kanwa ce ta kar tsami

kwannafi ya kwanta. Ya soma jin tausayin ta, kuma ya rage takura mata.

*****

RANAR KWANA BAKWAI

Ranar da auren su ya cika kwana bakwai ne komai ya faru, haduwar da rabuwar masu kama da *blink of an eye* (kiftawar ido). Gabadaya haduwar sa da saninsa da Raheenah Omar, zuwa auren su da zaman auren watanni uku ne cif har kwanaki bakwai na aure data yi a gidan sa.

A safiyar ranar tun asubah ta faki idon sa ta dauke masa mukullai, neman duniya yayi musu bai gan su ba, kuma baya so ta gane abinda yake nema kenan, don haka yaja bakin sa yayi shiru, kada ta gane bai rufeta ba tayi tunanin guduwa, shi kuma daga ranar ya fara

nadama, ya kuma alkawartawa ransa bazai kara kusantar ta ba sai bisa amincewar ta.

Sannan zai yi kokari ya koma yadda duk take son sa, wato namiji dan soyayya, mara gaggawa, loving, caring, romantic. Mai bin komai a sannu. Sex will be his last priority a rayuwar auren su. In ta kama zai je makaranta ya shiga aji ya zauna a koya masa yadda zai koyi zama da mata ne zai yi hakan, sakamakon wani irin *pleasant feeling (so na hakika)* tamkar maganadisu mai jan zuciya da ruhi da ya ji yana shigarsa a hankali akan RAHINAH OMAR daga daren jiya zuwa wayewar garin yau.

Wayewar garin data cika kwanaki bakwai da auren su.

Bata taba yarda sun kwana gado daya ba, in suka gama

damben su yayi galaba akanta anan kasan marbles da ya barta bata canza matsugunni, sai in ya fita ne taji yunwa zata kasheta take yunkurawa ta isa ga firji ta sha madara ta koma ta kwanta. Haka zata wuni kuka idan ta tuno karatun ta, da abokan karatun ta da Dadar ta. Yau ta dauke masa mukullai ne da niyyar zata gudu, kuma zata bar Jamus gabadaya.

Bai nuna mata bai ga mukulli ba, tana daga kwance inda take ya sunkuya ya ajiye mata kofin *tea*. Sai tiriri yake. Ta runtse ido hawaye na bulbula domin ko fuskarsa bata son gani. Kamshin turarensa duk ya mamaye ta. "Kiyi hakuri sweetie, i promised to become a changed person, if you give me another chance (nayi alkawarin canzawa, in har zaki bani dama). Yanzu

dai na makara, inna dawo zamu tattauna sosai".

"Allah yasa kafin ka dawo ka tadda gawata!"

Ta fada cikin rishin kuka. Tana mai addu'ar Allah ya dauki ranta ta huta kafin Habibu ya dawo

Murmushi Habib yayi, sannan ya sunkuya ya sumbaci bakin ta *lightly*. Wani abu da bai taba wanzuwa tsakanin su ba (sumba). Ta tattaro miyau ta tofa masa a fuska. Maimakon ta ga ransa ya baci ko ya falleta da mari kamar yadda ya saba, sai taga yasa dan yatsa ya lakato miyan ya kai bakin sa ya lashe.

Ya kuma kasheta da murmushi yace "i know that i offend you, and it's intentional as you expect, but i promised to become new HABEEB (masoyi) har sai kin koreni sabida

soyayya. Ki bani thirty minutes yanzu zan dawo we will discuss everything, in nace EVERYTHING ina nufin har ASALI NA da naki".

Maimakon maganganun sa su farantawa Raheena, sai ma suka kara shafa masa shuni a idanun ta. Ba abinda zai ce ta yarda yana kaunar ta. Ya baro gini tun ran zane....zuciyar ta ta riga ta mace a tsanar sa.

Abinda kuma zai farfado da matacciyar zuciyar nan ba kankani bane. Ya riga ya raunata zuciyar ya yi mata illah. Tsanar data yi masa ba 'yar kadan bace. Kuma zata nuna masa ita ba yar tsana bace duk rashin gatanta ta san 'yancin kanta.

Haka ya fita yana waiwayen ta, ita kam ko ido bata sake dagawa ta dube shi ba. Mintina goma sha biyar ta bayar bayan

fitar sa, ta mike tasa jallabiyya, tasa jilbab, sannan ta tattara duk wasu muhimman takardun ta da *passport* dinta ta fice cikin zafin nama.

*****

"Divorce (Scheidung) a kasar Germany: ba karamin abu bane. Domin tunda ke ke son sakin, sai kin dauki lawyer. Sannan zaki biya kusa €3,000 kudin kotu dana daukar lawyer. Ki rubuta application for divorce (divorce petition) in kin tabbatar kina da gamsassun hujjoji. Sannan ne za'a shiga family court a gudanar da sakin under German-law. Tunda dukkkannin ku kuna kasar Jamus. The divorce will run in accordance with German law regardless of your nationality (sakin zai kasance ne karkashin kundin

tsarin shari'ar Jamus batare da la'akari da kasancewar ku ba 'yan kasa ba).

However, also in this case, sai kin jira end of the one-year-separation before starting the divorce procedure".

Ambasadan kasar Najeriya a kasar Jamus yayi mata bayani cikin nutsuwa. Da gani yarinyar *is desperate*, sakin kawai take so ba tareda ta san aikin dake gaban ta ba, "tun farko me ya kai ki amincewa da auren sa in kin san ba kya son sa?" Ya tambaya *calmly*, Rahina ta sanya gefen jilbaab dinta ta goge gumi da hawaye, "ranka ya dade basu bani damata ba, uwardakina ta kasar nan ita tayi min fin karfi, hujjarta kakata tace kowa aka samu a aurar dani gareshi. Ni kuma ba na son sa, ban san shi ba, ban san komai a kan shi ba".

Ambasasada Shehu yace "zaki iya gaya min hujjojin ki na rashin son zaman aure? Idan har akwai ci da sha da suttura?"

Rahinah ta rasa inda zata sa kanta, da kunya ta fadi hujjojin ta, balle a gaban alkali. Me take so daga gareshi banda SOYAYYAH??? Asalin sa, da sanin dalilin sa na auren ta?"

Kuma a yau ya ce, tayi hakuri in ya dawo zasu tattauna komai *and he promised to become a changed person* irin yadda duk take son sa. What else take so daga gareshi bayan wannan? Ya riga ya dasa kiyayyarsa a zuciyarta ne ta yadda babu wani *repenting* da zai yi ya wanke dattin laifukan da yayi mata.

Ambasada ya ga shirun ta yayi yawa, yace "bazan iya tsaya miki ba, har sai na san hujjojin

ki masu karfi ne, sabida Jamus ba Najeriya bace, karshe a kare da cin ki tara. A yanzu haka ma in zai sake ki sai kin biya shi kudi masu yawa, *do you have any source of income* bayan alawus din ki na cin abinci?"

Rahinah ta kara rudewa, tace "ka taimakeni yadda Allah ya taimake ka, banida komai da zan biya shi, bani da kowa da zai kwatar min 'yanci. Shin rashin so bai zama hujjah ba? Bana son sa ne, kuma bazan taba son sa ba".

Ambasada Shehu yayi murmushi, ya gama gane wauta da tarin kuruciya a tare da ita, banda haka auren, ai shine rufin asirin ta. Kowanne iri ne kuwa. Don haka yace.

"'Ya ta, zan tsaya miki kamar Babanki, domin hakkin walwalar duk wani dan kasar

Najeriya dake Jamus yana wuya na, amma hujjar ki bata isa hujja da za'a kai kotun Jamus ba, sannan baki da kudin da zasu nema. Don haka in zaki bi shawara ta in ma sakin zaki nema to ki nemeshi ta hanyar sulhu saki na addini tunda auren musulunci kuka yi ba tareda kin kai shi kotu ba.

Ni zan kira yaron mu zauna mu uku, gara ya baki saki bisa doron musulunci tunda shi kika zaba amma ba ta hanyar kotun bature ba. Hakan zai jawo babbar matsala ga karatun ku ku duka, don dukkan ku ba abinda ya kawo ku ba kenan. Kuma in gwamnatin garin ki ta ji a inda kika kare a kotu zaki yi disappointing din ta ga kara *sponsoring* yara mata, sannan jami'ar ku zata shigo zancen wanda duka matsala ne ga

karatun ku. Don haka ki barni in ganshi mu zauna mu duka. Idan rabuwar ku ita ce mafi alkhairi ya sake ki ta ruwan sanyi bisa doron saki na addini".

Jikin Rahina yayi sanyi sosai, kuma tana hango rashin yiwuwar hakan a idanun ta; Habib bazai yarda ya sake ta ta ruwan sanyi ba, ta gama gane mutum ne mai naci akan abinda yake so, kuma hargagi ko barazana basa razana shi. Shiyasa ta so ta kai shi kotu. But who is she to argue with this humble ambassador?"

"Na amince a kira shi in roke shi ya sake ni, a bisa hujja ta bana son sa".

Ta fada cikin matsananciyar faduwar gaba, tana mai jin tamkar hukuncin data yanke bai yanku ba, kamar zai dawo

watarana yayi ta haunting din ta (evocative feelings).

*****

Da ya dawo daga aiki sai da ya tsaya yayi mata *take away* na abincin ma zafi, duk da ya san ba ci zata yi ba, wannan rashin cin abincin nata ya fara damun sa, in dai shine ya bar abinda bata so daga nan har gaba da shekara in dai zata hakura ta zauna da shi cikin aminci. Wanda a hankali yake fatan ya rikide musu zuwa soyayyar da yake tababar idan zuwa yanzu, bata fara aiki acikin jikin sa ba.

"Ka yi mata wani abu da zai sa ta farin ciki".

Zuciyar sa ta bada shawara. Sai kawai ya samu kansa da shiga supermarket, katittika na ban hakuri da kalaman soyayya masu tausa zuciya, masu kyau da

nagarta ya zaba tareda 'rose flower' mai dadin kamshi. Ya wuce gida yana mamakin kansa, ko dai Rahinah ta sa ya fara zarewa ne? Gabadaya albashin sa na yau ya karar da shi ne a sayi banza sayi hopi duk don ya farantawa Rahina ya fara wanke dattin sa dake ranta.

Amma me? Sama ko kasa babu Rahinah babu alamar ta.

Ba inda bai duba ba cikin gidan, ba inda bai bankada ba, kuma da ya zo ya tadda kofar gidan a bude, wannan ya tabbatar masa Rahinah ta gudu.

Gidan Dr. Laura shine ya fara fado masa a rai, don ya san bata da wani waje bayan (hall of residence) na dalibai sai shi. Cikin tsananin tashin hankali ya tari taxi zuwa gidan Dr. Laura.

" Ni rabo na da ita tun ranar da kuka bar nan, ba mamaki ta

gudu Nigeria, tunda dama ba son auren take ba".

Ji yayi gaban sa yayi wani irin mummunar faduwa. Ya bar gidan Dr. Laura ko gaban sa baya gani, hakan bai hana shi nemanta a (hall of residence) ba, inda abokan karatunta suka tabbatar masa tafi sati biyu bata zo ba tun da aka fada mata mutuwa daga gida.

Allah kadai ya san a yadda ya kwana ranar, yana safah yana marwa, har airport ya je ya duba bai ganta ba, kuma an tabbatar masa babu jirgin daya tashi zuwa Najeriya a yau. Yana so yayi reporting wa police yana tsoro don ya san *he don't have all the right to force her to marry him.*

Kafin gari ya waye Habibu har ramewa ya yi.

Sai a washegarin ranar ne ya samu kira daga Nigerian Embassy. Nan take hankalin sa ya kara tashi, ya tabbatar akan maganar ta ne, kara ta kai shi kenan! May be har kotu ta shigar. Tunda yake a rayuwar sa ba abinda ya tsana irin kotu. Balle a tsaida shi a mumbarin shari'ah a ganin sa karshen tozarci kenan. Auren sa duk lalacewar sa da take fadi garkuwa ne a gare ta, amma dakikiyar kwakwalwar ta ta kasa ganewa. *For the last time* ya ji yana son yi mata duk abinda take so don a zauna lafiya.

Ambasada Shehu ya dube shi sosai, *a perfect gentleman indeed*! Wanda ga dukkan alamu ilmi ya gama ratsa shi. Ko mai yasa matar sa ta kasa son sa a fannin aure? Ko da yake ba'a nan take ba, wasu mazan basu

rasa komai ba amma sun rasa dabarun tafiyar da diya mace, and they are very selfish akan bukatunta, wanda yake maida komai nasu ba komai ba a idanun ta.

"Habib Mustapha Nahuche, matar ka Raheenah ta zo min tana neman saki daga gare ka, a yadda ta zo min, a shirye take data je neman saki daga German Law. Ko kun san girman abinda kuka dauko a kasar nan kuwa? Me zai hana ku zauna ku gano matsalolin ku ku nemi hanyar magance su? Sai naga cewa a matsayin ku na musulmai haihuwar musulunci tashin musulunci sulhu ne ya dace daku. Was-sulhu Khair".

Rahinah ta zuqi numfashi ta fesar, tace "ranka ya dade bai aure ni ta hanyar da zan taba son sa, in dai rashin so hujja ce

babba data isa a raba aure akan ta, to bana son sa, ban taba son sa ba, kuma bazan taba son sa ba.....ta fada masa tun haduwar su ta farko a jirgi, da hanyar da ya bi ya aure ta a wulakance hannun su Dr. Laura wadda bata dauke ta a bakin komai ba. Amma ta yi ta yi ta fadi sirrin dake cikin zaman auren ta kasa, akan dalilin da bata sani ba, ta alaqanta hakan da kunya ta diya mace. Tace "na zo Jamus ne don nayi karatu, i'm goal oriented, ko zan yi aure ba yanzu ba kuma sai cikin mutunci cikin dangi na, mutuwar kakata bata nufin faduwa ta. Idan har da gaske kai ne uban mu a wannan kasa, ina rokon ka, ka dubi al'amari na da idanun adalci, ka karba min 'yanci na".

Ambasada Shehu ya maida duban sa akan Habibun, wanda

ya ji ya gama muzanta a idanun Ambasada. Ambassada yace "Habibu meyasa da gaggawa haka? Ko ka manta gaggawa aikin shaidan ce?"

Muryarsa ta yi kasa sosai, it's not easy a fada a fili ba'a son ka, bayan baka rasa komai da za'a so kan ba. Dadin shi daya ne yadda Raheenah ta boye sirrin dake cikin zaman auren su, ya san da dan sauran mutuncin sa ya gama zubewa daga idanun Ambasada.

"Ranka ya dade idan ta barni zan cutu, zan shiga wani hali, zan fada wata rayuwa daban da ba tawa ba, na dandana aure na san yadda yake, a matsayin ka na namiji kamana zaka fahimci abinda nake nufi, zamana ba aure babbar matsala ce a gareni yanzu. Ka dubi al'amari na da idanun dalci, ta fadi duk abinda

take so na yi, na yi alkawarin kwatantawa.

Nima na san ina da wasu *odd* dabi'u wadanda ta kasa jurewa. But i promised to become a changed person, a changed man for her, duk yadda take son na koma".

Da sauri Raheenah tace "saidai kai auri wata, ko dole sai ni? Idan ma ka ki saki na bazan taba komawa gidan ka ba sai dai akai gawa ta".

Habibu yayi mata wani fitinannen kallo, kafin yace "your excellency i will do as she wish, saki nawa zan rubuta mata?"

Ambasada ya dafe kansa, bai so hakan ba, ya so su yi sulhun, couple din look perfect together, kowannen su ya san ciwon kansa. Sannan shima yana *backing* aure kowanne iri ne sama da rayuwar da 'ya'yan

musulmi ke yi a kasashen ketare. Ya so ya ga laifin Habibu kan *method* din da ya bi ya auri Rahinah, wanda shine babban abinda ya ja masa kiyayyarta, sai ya ga cewa ko shine a matsayin Habibu bai da wata hanya banda hakan in dai yana son ta, *he can relate* dalilin sa na yin auren afujajan a matsayin sa na namiji, (don ya kaucewa zina ne) kuskuren sa daya gaggawa, ya aureta babu fahimtar juna.

Kafin ya samu abin ce musu su duka, Habibu ya dauki takardar dake bisa tebir, mai tambarin Nigerian Embassy Germany, ya zari biro a gaban suit din sa, ya rattaba saki a jiki, ya mikawa Raheenah.

Idanuwan su suka hadu, suka sarke na 'yan sakanni, sai ta ji hankalin ta na son barin gangar jikin ta. Ta kasa mika

hannu ta karba, *because she never expects him to do it so quickly*. A wurin Habibu kuma daga yau ya gama da babin Raheenah. Zai bude sabuwar rayuwa waadda babu mata da tunanin lamarin su cikin ta.

Ajiyewa yayi a gaban ta, ganin cewa ta gaza karba, ya nemi iznin tafiya daga Ambasada, Ambasada ya gyada kai cike da tausayin yaron, a cikin kwayar idanun sa ya gano kwantacciyar soyayyar Raheenah zallah. Amma *bravery* din da yaron ya nuna ya burgeshi. Fatan sa kada ya fada wata mummunar rayuwa bayan tasa, kamar yadda ya fada a baya.

Bayan fitar Habibu Nahuche, Ambasada Shehu ya dubi Raheenah wadda ke sharar hawaye, hawayen da bata san dalilin su ba; as she is supposed

to be happy, amma sai taji wani bangare na can kasan zucciyar ta baya farin cikin, ji take kaman ta yi *mistake* din da bazata taba iya gyarawa ba.

Ga dai 'yancin ta samu, na yin rayuwarta *freely* a kasar Jamus, aunty Laura tace zata iya zama *internationalprostitute*, wani matsanancin tsoro da firgici ya kamata, kodai auren Habibu GARKUWA ne duk da babu irin soyayyar da take bukata a cikin sa?

"This is what you want my daughter, what is your next plan?"

Ya fada *sounding fatherly,* kamar shi ya haife ta, bata taba samun soyayyar uba ba, sai taji wannan kulawa ta Amabasada ta bata dan guntun *hope* na ta cigaba da rayuwa, zata samu mai kulawa da ita bayan Dada, zata

samu kariya a karkashin kafadun sa, zata samu mafaka a karkashin alfarmar sa.

"Makaranta zan koma, karatu ya wuce ni sosai, zan dage ne in kamo abinda ya tsere min. Amma ina tsoro, ina jin tsoron zaman hostel sabida rayuwar da ake yi acan tana tsorata ni".

"Nayi miki umarnin zama cikin iyali na, idan har zaki tsare mutuncin kanki, ki kuma maida hankali kan abinda ya kawo ki kadai. Direban dake kai yara na makaranta zai din ga kaiki Cologne kullum yana dawo dake".

Raheenah don farin ciki sai ta fashe da kuka, ta gurfana gaban sa tana godiya, godiya mai tarin yawa, ta ji duk wata damuwa ta kare mata. *At last*

she will become what she want in life, Otorhinolaryngologist.

****

NEW PHASE

Komai na rayuwar sa ya tsaya masa cak, ya kira wajen aikin sa ya ce ba h da lafiya, kasancewr rubutun *thesis* din sa na M.Sc yake yi baya halartar *lectures*, amma a zahiri babu inda yake ciwo a jikin sa, ciwon a cikin tsokar dake tsakiyar kirjin sa yake.

Rahinah Omar! Rahina Omar!! Rahinah Omar!!!

Ta shigo rayuwar sa da wani irin karfi, ta yi tasiri mai yawa a cikin ta, ta yadda har ya soma tababar hukuncinsa, anya bai yi kuskuren da bazai taba iya gyarawa ba? Me yasa bai barta ta tafi duk inda take so da igiyar aurensa ba har zuwa ranar da Allah zai sake hada su? A lokacin da TA HUCE take ganin zata iya zama da shi kuma *goals* din ta sun zama *actualized*? Zuciyar sa nan da nan ta ce 'kalamanta ne". Babu namijin da zai iya jure kalmar rashin 'so' babu sakayawa na fita daga bakin matar sa a bainar jama'a. To idan so cuta ne, to hakuri ma magani ne, daga yau zai koyawa rayuwar sa juriyar rashin mace kowacce iri, koda kuwa ace da *gold* aka kera ta.

Ya soma tunanin watannin da suka rage masa ya bar kasar

Jamus ba masu yawa bane, zai yi kokari ya kammala *thesis* din sa ya koma gida, ya fara maida kobo ya koma dari, watakila mata mai kudi suke so, watakila don bata gan shi da mota bane, watakila don bai da gidan kansa, ko kuma watakila don abinda yake ciyar da ita da shi bai isar ta, tunda in dai akan maganar soyayya ne ai yayi alkawarin canzawa, meyasa bata bashi dama ba?

An taba soyayya rana daya ne? Wasu ma'auratan har su haihu basu gama fahimtar juna ba, ya kamata Rahina ta yi masa uzuri, uzurin da addini yayi wa musulmi umarnin sa har guda saba'in kafin su kama shi da laifin da suke tuhumar sa. kasancewar dukkan su bakin haure ne auren su ba zai zama kamar suna kasar su cikin

iyayen su ba. Yes, yayi gaggawa, but he has no option banda ya mallakawa ruhin sa abinda yake so don ya zauna lafiya. Ya kamata ta duba lamarin sa, ta kuma gane gangar jikin sa ce a bukace da aure a lokacin ba soyayya ce *priority* ba.

In da ta yi hakuri, *along the way* soyayyar na zuwa kamar yadda ta zo ta lullube shi a halin yanzu.

Kwanan sa bakwai bai fita koina ba, yana jinyar da bata ciwon jiki ba a'ah, jinyar zuciyar da soyayya ta riga ta yiwa illah, amma ya yi alkawarin *overcoming* din ta da addu'a da jajircewa *by been stronger,* ba don kudin *rent* da yake biya ba barin aikin zai yi, ya dukufa wajen karasa *proposal* din sa.

Ya alkawartawa ran sa ba shi ba Raheenah, koda ita ce

autar mata, ba zai kara zuwa inda ta ke ba, ko a hanya ya ganta zai dauke kai, ta je ta yi rayuwar ta yadda ta zabeta.

Wani sako na zuciyar sa na tabbatar masa da cewa watarana in ta gama bokon nata, *when her dreams are born alive, she will surely come to* sanin cewa ta yi sake da damar ta a baya, *she will come searching for love* wanda a lokacin zai yi mata wuyar samu.

Yes he accepted the fact* cewa bai kyautawa Raheenah Omar ba, a takaitaccen zaman auren su, amma kuma wanene yake sama da kuskure? Sai aka yi mana umarni da in mun zo gyara kuskuren mu a bamu dama, koda itace *one last chance in the whole world.

Allah da Manzon sa sune kadai suke *perfect* a komai, shi dan adam ne, *he must have his*

***own flaws*. A yayin ne kuma wani tunani ya darsu masa, ko dai Rahinah bata da lafiya irin ta 'ya'ya mata ne? *She never appreciates* auratayya. Kuma kamar ma shine abinda tafi tsana a rayuwar ta.**

Akwai mata masu irin wannan halittar sosai, wanda ba ciwo bane halitta ce, only caring husbands can understand and go along with them as such. In ba haka ba ina dan adam zai zabi boko akan sunnar Annabi? Koma dai menene shi an yi ta ta kare tare da shi, taje ta ji da bokon ta, in ta so ta zamo farfesa.

A dare na uku, ya soma samun sassaucin zuciyar sa, ya cire tunanin sake aure daga ran sa. Ya soma haka wani wawakeken rami domin binne

Raheenah a ciki ba don ta mutu ba, sai don ya samu sa'ida wajen gudanar da al'amuran cigaban rayuwar sa.

Sai a washegari ya samu kiran Hajiyar sa, Haj. Kaltume Nahuche. Bai san dalili ba yana jin kamilalliyar muryar ta cikin kunnuwan sa sai ya samu kansa da saka kuka. Shi autan ta ne, ita kadai yake sakewa da, amma ko ita bai gaya mata auren da yayi ba, ba don komi ba sai don ya san bazata amince ba, kuma bazata taba bari ya auri yarinyar da basu san asalinta ba, *besides*, ta dade da kama mishi mata a cikin dangi.

"Hajiya kiyi min addu'a, ina cikin wani hali"

"Ko minene Allah ya sawwaka shi, ya zaba abinda

yafi zama alkhairi, saura wata nawa ka dawo? Don asa bikin ka da Shafa'atu kurkusa. Kana dawowa sai ta tare, in ya so daurin auren sai a yi ba sai ka dawo ba".

"Hajiya ayi hakuri kawai, in ta samu miji ta yi aure. *I've nofeelings* akan diya mace yanzu, an sha ni na warke, sai fatan cikawa da imani".

Zuciyarta ta narke, jin yadda yake magana *in despair*, la shakka wata ta karya zuciyar autan ta.

"Wacece ita? Kuma a ina take? Su waye iyayen ta?"

Ta jero mai tambayoyin guda uku a jere kuma a tsanake, Habib ya kwantar da kai akan masangalin kujerar falon sa, bai taba boyewa mahaifiyar sa komai na rayuwar

sa ba, sai auren sa da Raheenah, kuma fada matan a yanzu bashi da wani amfani tunda auren ya riga ya narke, *with no any form of bright memories.*

"Sunan ta Rahinah".

Hajiya Kaltume tayi shiru, kafin tace "menene tsakanin ku? Habibu bana son kwashe-kwashen bariki, ka maida hankali ka gama abinda ya kai ka ka dawo gida, ka auri 'yar uwar ka cikin rufin asiri, matan nan na kasar waje duk yawancin su kyal kyal banza be (kyau ba hali). Ba ana aure don kyawu bane ana duba asali (nasaba) da nagarta. Nikuma shine abinda nake bukata a matar auren ka, wanda duk 'yar uwar ka Shafa'atu ta hada. Idan kuma arziki ka hango a jikin ta

wannan na Allah ne, rabon bawa kuwa zai tadda shi har inda yake".

"Hajiya ta maganar bazata yiwu ta waya ba, amma na yi alkawarin duk ranar dana dawo gida gabadaya zan gaya miki duk abinda ya faru. Ina fatan a ranar kiyi min uzuri ki karbi hanzari na".

Haj. Kaltume bata ce komai ba, bayan "Allah ya bamu mafita ta alkahairi".

And so it was.....addu'ar uwa bata faduwa kasa banza, domin ya samu mafita a cikin addu'ar ta, ta karfin zuciya (courage) da karbar rayuwa a duk yadda ta zo masa.

****

Gidan Ambasadan Najeriya a kasar Jamus babban gida ne (family house) mai dauke da

matar aure daya Nene Bilki da yaranta biyar maza hudu da mace daya Safeenah. Itace babba sai kannen ta hudu 'yan maza; Safwan dan ajin karshe a sakandire, sai Abbas mai bi masa yana aji hudu, Suhaim da Ahlan sune kanana 'yan firamare a gidan. Kenan Safinah ita ce kadai tsararta a gidan duk da cewa ta bata a kalla shekaru biyu, shekarun ta 21, tana mataki na uku a jami'ar *Goethe University,* Frankfurt.

Nigerian Embassy yana Frankfurt, daga Frankfurt zuwa Cologne tafiyar mota na awa biyu ne, wato 118 miles ko 180km. Amma haka Ambasada yasa kullum ake dauko Raheenah a motar gidan sa zuwa makaranta, in an sauke su

Safwan itama a kaita har Cologne, karfe 6 azo a dauketa.

Zaman ta da iyalin Ambasada Shehu kadaran-kadahan, rayuwa ce ta ba ruwan kowa da kowa kuma kowa yana da abin yi da zarar gari ya waye, daga nan kowa zai kama gabansa wajen neman ilmi masu aiki su tafi aiki, wato Nene da Daddy, yaran duk a kai su makaranta kuma sai yamma suke dawowa a tare, idan direba ya fara dauko Raheenah sai ya zo ya dauki wadanda ke cikin gari, Frankfurt.

Akwai mahaifiyar Ambasada a gidan da suke kira Yafendo, kusan da ita jinin Raheenah ya fi haduwa duka gidan, sabida tana da halaye da dabi'u irin na Dadar ta. Su murza goro a magogi, kadin

auduga, yawan girki, sannan bata cin girkin kowa ita take dafa abun ta na gargajiya, kullum in ta dawo makaranta tana son hira dakin Yafendo take tafiya, in kuma tana da karatu ko assignment to tana dakin ta. Safeenah jinin su bai hadu ba sam, saboda ta faya kishi, yadda take ita kadai mace a gaban iyayenta rana daya Daddy ya kawo wata tsarar ta ya ajiye musu a gida don kawai yana uban 'yan Najeriya a Jamus.

Gaisuwa kadai ke shiga tsakanin su da Safeenah, dakunansu na kallon na juna amma ba mai shiga harkar kowa, ita kam Nene akwai faram-faram kamar mijin ta, tana aiki a Frankfurt Airport. Amma bata jan baki a jiki,

sama-sama dai, kowa yayi zaman kansa.

Babban abokin ta a gidan kam auta Ahlan ne, da suke yawan haduwa a dakin Yafendo. Abinci ba matsala bane a gidan, duk abinda kake so akwai a kicin in bazaka ci wanda kuku ya girka ba. You are free to cook. Wannan sune sabon family din da Rahinah Omar ta tsinci kanta cikin su. Tana kuma jin dadin zama dasu da dukkan zuciyar ta, musanman halayen su na rashin sa ido. Kowa a gidan *goal-oriented* ne.

****

Tayi sallama a dakin Yafendo, ta sameta tana kadin auduga, Yafendo tayi mata murmushi ta ce "har an dawo? To ga kwadon rama nan na ajiye miki, duk sanda muka je

gida nake yo guzurin abuta busashshiya mai yawa in aje, in naji kwadayi in jika abata ta sha kuli kuli shikenan".

Ji tayi wani mugun yawu ya tsinke mata, tsabar how eager ta zama ga cin ramar, ta ja kwanon da sauri ta soma aikawa cikin ta.

Yafendo tace "bani labarin ki mana jikata? Iyayen ki 'yan wane gari ne?"

"Iyayena 'yan Girei ne Yafendo, amma ban taba ganin su ba sai a hoto, sunan Babana Malam Omar Modibbo, mahaifiyata Bingel ake ce mata bansan sunan ta na gaskiya ba, duk sun rasu ina karama a hannun kakata na girma, a sani na ita zan iya kira iyaye na saboda ban san dadin kowa ba sai nata".

Yafendo tace cikin mamaki "Girei ta Adamawa?" Tace "nan fa""mun taba zama ci rani a garin nida miji na kasancewar sana'ar kiwon shanu yayi, gari ne mai dadin zama, yaya sunan Kakar ki? Don akwai Umaru Modibbo dana sani a garin mai mukamin Sarkin Fulanin Girei aboki ne ga Baban Ambasada domin yana sayen shanu wajen sa".

Cikin tsananin faduwar gaba Rahinah ta ce "har yanzu 'yan uwan sa suna Girei?""Eh toh bana ce ba, tunda mu zaman dan lokaci muka yi a garin, mun san shi a matsayin sarkin Fulanin Girei, amma yaya sunan Kakar taki?""Sunan mu daya, Rahinatu, sunanta aka sanya min. Ana kiranta Dada""ai ko dai sune wadanda

na sani, ita Dada tana sayar da daudawa da man shanu kuma na kan saya a wajenta, kuma a lokacin da na santa ba Umaru ne kawai dan ta ba, tana da wasu yayan biyu, ta taba gaya mun Daya yana Kaduna da iyalin sa tunda ya tai karatu birni ta rasa shi, daya ta mutu wajen haihuwar Farko, amma dai na san in aka je Girei zaa samu cikakken bayani a kan su tunda sarkin Fulani ba boyayye bane, to amma kin ce a garin Adamawa kika girma, su kuwa a Girei na san su" da sauri Rahina ta mike tana fadin bari in nemo miki hoton Dada ki tabbatar min idan ita ce don Allah Yafendo""wannan abu mai sauki? Idanun nan nawa duk yawan shekaru da tsufa ras suke. Ba abinda bana ganewa"

kafin ta rufe baki Raheenah ta fita a dakin.

Ta jima tana bincike a cikin kayan ta, ta hargitsa komai na dakin ta, kafin ta samo hoton su ita da Dada tun tana karama, tsabar dadewar hoton ma na farar kala ne. Ta dawo ta kawowa Yafendo, gabanta na wani irin faduwa da fargabar abinda Yafendo zata ce.

Tsohuwar ta kura ma hoton ido, kafin tace.

"Wannan Rahin ce, tabbas Rahin ce babar Ummaru,,,," Rahina ta saka kuka tace "don Allah ki kai ni garin in nemi dangina, Dada bata taba gaya min komai a kan su ba, banda cewa da tayi iyaye ne sun mutu, itama daga baya ta rasu.

Nikadai ce bani da kowa a duniya.....".

Yafendo ta kamata ta rike tace "daina kuka 'yar nan, insha Allahu da kaina zan kai ki har garin Girei, kuma zan sa Ambasada yayi bincike mai yawa idan mun je gida, duk shekara muke zuwa ganin gida, yanzu bamu jima da dawowa ba amma da zarar zamu je har da ke zamu tafi, ki kwantar da hankalin ki, kinsan 'yan bokon nan ba abinda basa iya bincikowa".

Da haka ta samu ta lallashi Rahinah, suka yi sallama ta koma daki cike da zullumi.

A daren bata yi wani isashshen barci ba sabida taraddadi da ya cika ranta, ashe tana da rabon ganin wanda zai ce ya san wani nata ma bayan

Dada? Excitement ya cika zuciyar ta, ta dokantu shekara ta zagayo ta bi iyalin gidannan Najeriya.

Washegari da safe ta yi shirin makaranta, ta hada tea a dining din kitchen zata sha, kawai sai taji zuciyarta na tashi kuma ba abinda take so sai ramar Yafendo.

Da sauri ta suri jakar ta ta nufi dakin Yafendo. Ta idar da sallahr walha kenan, ta shigo dakin kamar an jefo ta, "Yafendo don Allah don annabi ki sammin rama da kuli, in ban ci ba yanzun nan mutuwa zan yi".

Yafendo ta katse lazimin ta jin abinda Rahinah ke cewa, kafin kuma ta bata amsa ta hau daddaga shirgin Yafendo tana neman Ramar, Yafendo tace

"Rama da safiyar nan 'yar nan? Ki tafi makaranta kafin ki dawo zan kwada miki, yanzu ki nemi ruwan dumi ki zuba a cikin ki""na hada na kasa sha, tashin zuciya bambita yake sa ni, don Allah ki taimakeni".

Da sauri Yafendo ta dauko ramar, tace "jona ruwan dumi a butar can" cikin minti biyar tayi mata kwadon ta bata.

Nan ta hau ci ba kakkkautawa hannu baka hannu kwarya. Yafendo tana ta mamaki a ranta, anya lafiyar ta?

Data dawo daga makaranta ma kai tsaye dakin Yafendo ta zarto. "Na kwaso yunwa Yafendo, zan samu kwadin ramar ki?' Kawai sai ta ga Yafendo ta zaro kwano a rufe ta

mika mata, already ta kwada tun kafin ta dawo".

"Allah ya kara nisan kwana Yafendo nagode" ta soma ci a urunce. Yayin da Yafendo ta tsura mata ido.

Ta koma dakin ta ta sunce zata yi wanka, amma sai ta bige da kallon kan ta a mudubi, a take ta hango wasu bakin sauyuka a halittar jikin ta. Abinda ya fi daukar hankalin ta shine karuwar girman kirjinta sosai, sannan tayi wani irin fari dau! Kamar babu jini a jikin ta.

Rahinah bata damu ba ta cigaba da wankanta tana fadin mutum na kara girma ai dole kirjin sa ma ya kara girma.

Tana fitowa Ahlan ya shigo da gudu, "Aunty Rahina Nene tace wai yau baki ci abinci ba ko lafiya?" Ta ce "Ahlan ka

gayawa Nene wallahi kwanan nan ban iya cin komai sai RAMA".

Ba jimawa sai ga Nenen da kanta, tayi sallama ta shigo, tace "Rahinah me kika ce a gaya min? Ban gane hausar Ahlan ba, Jamusanci ya masa yawa" nan ta maimaita mata. Tace "ke a ina kika ga Ramar?""Wajen Yafendo, tana da ita mai yawa" Mami ta tsura mata ido, a take ta hango sauyukan data ke son gani. Tace "Rahinah kina yin period kuwa?" Kanta tsaye ta amsa "ai ni rabo na da shi har na manta, amma kin san *i'm too busy to notice that* ba don kin fada ba".

Nene tayi mata kallon tausayi, sannan ta ce yanzu idan ramar ta kare ya za'ayi?"

"Nima ban sani ba Mami,na dai san in ina so ban samu ba mutuwa zan yi, yanzu kam na koshi sai kuma gobe in Allah ya kaimu".

Mami ta juya ta fita tana fadin "on weekends zaki raka ni asibiti, mutum baya *period* ai gara a duba shi a san dalili".

Cikin damuwa tace "Nene, *is there any problen with that?*" Nene ta dafa kafadarta tace "*don't worry*". Sannan ta fita.

Nene ta ce kar ta damu, amma sai ta ji ta damun, ko wata cuta ce rashin yin *period* din?

Nene na fita dakin Yafendo ta nufa, ta samu kujera ta zauna, tace "Yafendo ko kin lura da abinda na lura da shi game da yarinyar nan?"

Yafendo ta ce "kwarai kuwa, kallon ta kawai nake, in kuma jira in ga ko zaki kula da kiwon da Allah ya baki. Shi aure dama in Allah bai nufi karewar sa ba wa ya isa ya karar da shi? Da zata ji shawara ta gara mata ta koma gidan mijin ta ta cigaba da hakuri irin wanda kowacce mace ke yi a gidan auren ta, ba namijin da yake cikakke a komai dukkan su suna da gibi, amma yadda na lura tafi jin dadin rayuwar ta da mu a haka bata ko so a dago mata zancen sa". "Kwarai wannan haka ne, bari in je in samu Daddy muyi magana a kan ta".

Yana sauraron radio Jamus a 'yar karamar rediyon sa lokacin da Nene tayi sallama ta

shiga. Ya amsa mata, sannan ta samu gefensa ta zauna.

"Ranka ya dade magana ce ta kawo ni, akan yarinyar nan Rahinah".

Ya rage sautin rediyon sa ya bata hankalin sa. "Ina zargin ciki ke gareta". Radeyon hannun Ambasada ce ta subuce kasa, tace "wallahi alamu sun gama nunawa, amma duk da haka ban tabbatar ba""kuje asibiti a tabbatar pls" Mami tace "insha Allahu, amma in ya tabbata cikin ne yaya zamu yi da ita ga karatun ta mai tsayi?" Ambasada ya nisa yace "yadda zamu yi da Safeenah, idan irin haka ta same ta".

****

Rahinah bata san me ta rako Nene yi a asibiti ba, amma tunda suka zauna a gaban likita

ya kuma ce ta bashi fitsarin ta komai ya fara kwance mata.

As a medical student ta san awon fitsari na nufin abubuwa da yawa.....awon cuta ko awon ciki! Don haka kafin sakamako ya taddasu, ta yi ligib cikin tashin hankali da tararradi.

"She's two months pregnant". Likita ta fadawa Nene ita kadai, bayan ta ce Raheenah ta je *reception* ta jira ta. Sannan ya bata shaidar hakan a rubuce.

Nene ta yi masa godiya, sannan ta fito ta tadda ita suka tafi, a hanya take gaya mata an ga shawara (jaundice) cikin fitsarin ta.

Raheenah tayi wani ajiyar zuciya, *feeling relieved*. Har suka zo gida zancen rama take wa Nene, wai yanzu idan ranar

Yafendo ta kare ina zata sa kanta? Nene tace "sai ki ci salad, ai shima ganye ne""amma bai da dan tsami-tsaminnan kamar na rama" murmushi Nene tayi, tace "sai a masa vineger".

Suna sauka a mota kuwa ta tafi dakin Nene cin rama.

Kwana bakwai kenan bata iya cin komai banda ramar, har yau gashi rama ta kare, babu kuma inda za'a sameta a Jamus.

Don haka tun safe take cikin kunci, haushin kowa ta ke ji, da Ahlan ya shigo yana mata surutu sai ta shige toilet ta rufe kanta don bazata iya korar sa ba.

Nene ta shigo dauke da plate a rufe ta sameta, "Rahinah yau bazaki makaranta bane? Yara duk sun fita sun

barki, ga wannan ko a mota sai ki ci kada ki tsaya ci ki makara, kin dai san kina da nisa".

"Nene yau ban iya zuwa makaranta" ta fada hawaye na ciko idon ta. "Sabida me?""I'm not feeling well, sabida tun jiya ban ci rama ba, Yafendo ta ce ta kare""try this" ta fada tana mika mata *plate* din hannun ta.

Bata yi musu ba ta karba ta bude, salad ne Nenen ta hada mata da kanta, yaji kuli da vinegar da tumatur, cocumbrr da albasa. Wani mugun yawu ya gudana a bakin ta, ta karba tun daga tsayen ta soma ci kafin ta zauna. Amma ko loma hudu bata yi ba ta dinga kwaro amai kamar zata amayar da hanjin ta.

Tun daga ranar komai ta ci sai ya dawo, ta galabaita

matuka, karfin jikin ta ya yi kasa sosai. Ambasada yace da Nene ta kaita asibiti, koda taimakon da zasu yi mata abinci ya dinga zama a cikin ta.

Suna asibitin likita ya riketa, domin yace she's 60% dehydrated. Aka sa mata *drip* nan take. A ranar ne Ambasada ya kira Habib a waya.

"In ka samu lokaci kazo 'Sachsenhausen Hospital' da daddare ina son ganin ka". "Insha Allah i will". Ya fada cike da girmamawa.

Karfe takwas na dare a Sachsenhausen ta yi wa Habibu Nahuche. Yana sanye da Native Hausa Attire dinsa na shadda sharaton ruwan makuba, ya kafa hula a gaban goshin sa ruwan toka mai turuwa sosai (deep grey), yayi kyau kamar

koyaushe amma kallo daya Ambasada yayi masa ya gane muguwar ramar da yayi cikin watanni biyu da yayi bai ganshi ba.

A wajen parking motoci suka hadu, direba ya sauke ambasada, shikuma taxi ta sauke shi. Ambasada ya bashi hannu sannan tare suka taka zuwa dakin da aka kwantar da Rahinah. Daga ita sai Nene a dakin. Kamshin turaren sa ne ya fara shiga hancin Raheenah, wani kamshi mai tasirin da bazata taba mantawa ba....da sauri ta juya kai zuwa bakin kofar shigowa. Idanun su suka hadu, wanda hakan ya haifar da wani irin shock ga Rahinah dake kwance, domin ta ganshi ne ba zato ba tsammani.

Yayin da Habibu Nahuche ya tsura mata ido, gabadaya ta zabge ta lalace, maimakon ya zo ya ganta very healthy and jovial tunda ta samu rayuwa yadda take so? Ta karbi 'yancin ta da take ikirarin ya danne mata? Banda girman idanun ambasada da yake gani babu abinda zai sa shi amsa wannan kiran, don bai ga dalilin sa ba. Tunda komai ya kare a tsakanin su.

"To zauna mana kun tsaya kuna kallon-kallo kamar zakaru" Ambasada ya furta masa sounding fatherly. Ya nemi guri can nesa da gadon da take kwance ya zauna. Wani irin abu na hankoro a zuciyar sa, ta shiga bugawa fat-fat-fat, bai san idanunsa sun yi kewar ta ba, sai yanzu da suka ganta

kwance a gaban su, hatta zuciyar sa neman fitowa take daga tsakiyar kirjin sa....shikadai ya san halin ragaitar da ya samu kansa cikin wadannan watannin biyu masu kama da jiran tashin alkiyama a gare shi.

Rahinah ta dauke kai daga kallon sa, ta mayar wani gefen daban, tunda suka rabu ko sau daya bata ji kewar sa ba. Bai bar mata wani abun tunawa a zaman da tayi da shi ba na kwanaki bakwai, banda kyakkyawar fuskarsa ta Rumawa data zauna a zuciyarta ta ki fita.

"Na kira ka ne Habib, don in sanar da kai Raheenah na da ciki na watanni biyu".

Daga Habib har Raheenah, a tare zuciyarsu tayi wani irin

dokawa, ta doka ta sake dokawa ta ci karo da bango. Idanuwan Rahinah kamar zasu fado kasa.....jin maganar tayi tamkar saukar aradu a kunnuwan ta, zata rantse ko mutuwar Dada da aka gaya mata a waya bata firgitata ta ruda ta kamar abinda Ambasada Shehu ya fada yanzu ba...

Yayin da Habib, Mustapha Nahuche ya wani irin lumshe idanunsa.

Wani albishir ne zai ce ko bushara da ba'a taba yi masa kwatankwacin sa ba.

Wani irin maganadisu ya ji yana fizgar zuciyar sa akan Raheenah da abinda ke cikin ta..

The feeling is so sweet da bai taba jin mai dadi a zuciyar

sa kamar sa ba...nitsatstsen SO!

A hankali ya bude idanun sa akan Raheenah, wadda ta tamke nata idanun tamau, hawaye na zirara ta gefe da gefen su.

Which means she's not happy at all, she's *mourning* kaddar da ta afka mata rana daya.....ta tabbata ta rasa farin cikin ta daga yau, bata ga amfanin sauran rayuwar ta ba..

Ashe dai ta yi gudun gara ne ta tadda zago..... Habib Nahuche bai shigo rayuwarta don ya fita a lokacin da take so ko yake so ba.

Kaddara bata kare tsakanin su ba, mai hada eternal dangantaka ya riga ya hada wato gamayyar jiki, wadda a yau ta maida ita matar Habib

a karo na biyu har sai ta haife masa dan sa ko 'yar sa wanda take jin ba abinda ta tsana a duniya sama da kawo shi duniya...

A fili ta fada ".....bai yi sa'ar mahaifi ba, he's but selfish by nature wato mutum ne mai son kan sa da yawa (tana nufin Habib din).

Muryar Ambasada Shehu ta cigaba da ratsa mugun shirun da ya ratsa kamar daukewar ruwan sama. "My dear Son and Daughter isn't it high time you reconcile? Tunda kun ga yadda kaddara tayi daku, kowanne Da yana burin ya tashi tsakanin iyayensa biyu, broken home shine babbar matsala ga tarbiyya da rayuwar kowanne yaro, rayuwa duka 'yar afuwa ce, in kuka afuwantawa

juna kuka kuma zauna kuka gano matsalolin ku i'm sure zakuji dadin zama da juna tunda har ga rabo a tsakani...".

Habibu yasa hanky dinsa ya goge gumin fuskarsa da hawayen da suka cika masa ido, wadanda yake da tabbacin na farin ciki ne. Ya dubi Raheenah wadda ta kautar da kai gefe tana jin tamkar Daddy na diga mata narkakkiyar dalma a kirjin ta da ya ce wai ta komawa auren Habibu. Ya ce "ranka ya dade ni bani da matsala da hakan in har ta amince, abinda ba zanyi ba shine sake zaman aure da ita ba tare da amincewar ta 100% ba".

Rahinah ta juyo a hankali zuwa side din da yake, a hankali ta ce "to in dai ko

amincewata kake bukata to har abada bazamu koma ba, once beaten twice shy. Ba ciki ba ko 'ya'ya goma ne suka bayyana tsakani zan baka abin ka, yadda bana son ka haka bana maraba da duk abinda ya fito daga jikin ka...."

"Rahinatu!"

Ambasada ya kira ta sounding fatherly, "banda cin fuska ga wanda ya girme miki, balle mijin auren ki, wanda har yanzu kike cikin zummar auren sa, har sai idan kin haihu bai ce ya mayar dake ba. Tunda baki amincewa komen ba shikenan, amma ki janye munanan kalaman da kika yi masa".

Tana kuka sosai, kukan kaddarar da ta sameta, tace "ka yi hakuri Daddy na maida

kalamai na, amma har abada bazan koma masa ba".

"Shikenan zance ya kare, shima cewa yayi ai in kin amince. Kinga kuwa yasa tagociya kenan ga maganarsa. Don haka ki kwantar da hankalin ki kina hannun Daddyn ki, har Allah ya sauke ki lafiya".

Ya juya ga Habib, wanda tuni ya mike tsaye ya zuba hannayen sa cikin aljihun caftan din shi yana nufin barin dakin don in ya cigaba da zama zuciyar sa na iya fashewa ko tayi bindiga, a yiwa uwarsa da 'yar uwar sa asara! Ya gama saduda Rahinah bata son shi, kuma har abada bazata so shi ba, tunda rabon bazata da Allah ya kaddara a tsakanin su bai sa ta so shi din ba. Ya sha jin ance

mace na fara son mijinta ne daga lokacin da rabo ya gifta a tsakanin su. Wanda ke nufin ita Rahinah is exceptional and extraordinary daga sauran mata.....

"Daga wannan watan zaka dinga raba albashinka biyu kana bata rabi don ciyarwa har sai ta sauka. Ba don bazan iya daukar dawainiyar su ba sai don in baka damar ka ta uba da addini ya baka. Ka kuma koyi daukar *responsibility* na iyali tun daga yanzu".

Kansa a kasa idanunsa sun kada sun yi jazir yace babu damuwa insha Allahu. A turamin account number din ta".

"Kana iya tafiya Habibu, Allah yayi muku albarka, yasa

hakan shi ya fi alkhairi tsakanin ku".

Hawayen da yake ta rikewa ne suka kwace masa, ya juya kadan ya dubi Rahinah wadda ke kallon bayansa a lokacin, suka kuma hada ido, ji tayi zuciyarta na son karyewa (rauni irin na diya mace) amma ta amince wannan shine *decision* mai kyau ga rayuwar ta.

Sai ta maida idanunta ta lumshe su a hankali. Tana sauke ajiyar zuciya.

Shikuma yasa kai ya fita daga dakin, babu ko waiwaye. Kamar yadda yake ji a ransa bazai kara waiwayar RAHINAH OMAR a rayuwar sa ba.

****

Sai da ta kwashe kwanaki bakwai kafin ta samu karfin jikin ta, kuzarin jikin ta ya

dawo ko ba duka ba. Har tana jin zata iya zuwa makaranta a gobe monday.

Tana canza kayanta na barci zata kwanta Nene tayi sallama a dakin. "Rahinatu kin yi barci ne?""Yanzu dai nake shiri Nene""to zo mu yi magana irin ta uwa da 'ya" tayi murmushi, don Nene ta canza mata bakidaya tundaga samun cikin ta, sosai take janta a jiki yanzu, tana tausaya mata, domin gani take tayi kankanta da haihuwa kashin jikin ta kamar bai gama kwari ba. Sabida bata da manyan barage.

Ta zauna daidai kafar Nene Bilki ita kuma tana daga saman gadon ta, tace "Rahinah meyasa bazaki koma gidan mijin ki ba? Yaron nan ya bani tausayi sosai, da gani yana bukatar ki cikin

rayuwar sa. Can you be open to me? Inaso in san meye matsalar ku? A matsayina na uwa zan iya bada shawara".

Rahinah ta sunkuyar da kai, tana tuno irin rashin tausayi da rashin soyayyar da Habib ya gwada mata, kullum tana ji a littafai cewa aure abu ne na soyayya, miji tarairayar matarsa yake yana bi da ita ta hanyar da bazata cutu a shimfida ba, amma Habib Nahuche a wannan fannin sai dai a kira shi NOVICE. Don haka bata ga amfanin zama dashi ba gara tayi rayuwarta single.

Amma ta yaya zata iya gayawa Nene haka bata ga rashin kunyarta ba? Ita a ina tasan yadda ake rayuwar aure tunda ba taba yi tayi ba! She's

just comparing and imagining. Don haka ta ga gara ta rike sirrin auren ta a zuciyarta, shi ciki ba anyi shi don cin tuwo ne kadai ba. Ta soma tunanin abinda ya kamata ta gayawa Nene, don ita duk wata shawara in dai akan ta komawa Habib ne to bata bukatar ta.

"I don't love him Nene!"

Ta fada tana hawaye. "Sabida bai aure ni cikin mutunci da daraja ba, ya sameni a arha da yawa. Cigaba da zama dashi zai iya janyomin psychological depression".

"Allah ya sawwake" inji Nene Bilki, amma daga nan zuwa ki haihu ki nutsu ki fahimci zuciyar ki. Maiyiwuwa wani bacin rai ya sanya miki wanda ya lullube soyayyar. Bazan takura sai naji ba don

tsakanin mace da mijinta sai Allah da ya halicce su. Amma shi AURE is not all about love my dear.....so many cirmustances na sanya mu zaman aure. Ni kinga so nake Saffenah ta samu mijin amma Allah bai bata ba, shikuwa Habibu har cikin kwayan idanun sa na hango SO mai yawa, wanda nake da yaqinin da zaki hakura ku koma zai isheku rabawa ku duka, ya yalwaci zuciyar kowannen ku.

Yanzu mu bar maganar kome, mu yi ta karatun ki.

Kinga dai position din jikin ki na da dana yanzu ba daya bane, ba zaki jure wannan zirga-zirgar tsakanin Frankfurt da Cologne ba. Don haka na kawo shawara me zai hana ki nemi iznin accessing lectures

dinki online? In yaso lokacin jarabawa sai kije ki rubuta, doctor yace kina bukatar hutu sosai. In yaso in kika haihu sai ki cigaba yadda kike yi".

Rahina bata so ya zamo cewa kowacce shawara da Nene ta kawo bata dauki ko daya ba, banda haka da ta gaya mata……gara ta cigaba da zirga-zirga yadda cikin zai jijjigu ya bare. Cikin da bata maraba da shi ko kadan cikin rayuwar ta.

"To shikenan Nene, insha Allah zan rubuta application na neman iznin hakan, sai a karbo takardar asibitin" Nene tace "hakan dai ya fi".

"Sai maganar abinci, duk abinda kika je shi kike so, shi zuciyar ki ta kwanta da shi, kada kiyi kauron baki ki

gayamin, nikuma insha Allahu zan dafa miki muddin ina gida, in ma bana nan ga Yafendo, kada ki dinga zama ke kadai idan ba karatu kike ba". "Nagode, nagode Nene, Allah yayi muku sakayya da alkhairi, yadda kuka dubi maraici na Allah ya dubi haular ku a bayan ku".

****

Sati uku kenan tana karatun ta conveniently online. Natsuwa ta soma shigar ta yadda ya kamata. Tunda bata ganin Habibu A. Bilyamin Nahuche bata da bacin rai, kuma bata da damuwa.

Ciki dai har mantawa take yana makale a jikin ta, in banda mugun kwadayi da yake sa ta, kamar ta cinye Nene da

Yafendo sabida dafa min kaza, dafa min kaza.

To haka rayuwa take, komai lalacewar zamani baka rasa mutane na kwarai masu zuciyar taimako saboda Allah, iyalin Ambasada Shehu Bichi, ba abinda zata ce dasu sai addua da fatan Alkhairi.

Hutun farko na summer mutanen gidan duka zasu je Paris, amma Ambasada yace banda ita da Yafendo, su zauna suyi kadin auduga a gida, ta sha jarabawa tana bukatar zaman waje daya ta nutsu, don su kam in sun tafi sai sun kwashe sati hudu suna yawo.

Sun tashi ranar lahadi, gidan ya rage daga ita sai Yafendo, don haka ta lokewa tsohuwar, ba hirar data ke so su yi sai ta garin Girei da

mutanen cikin sa. Duk yadda Yafendo ke son ta nusar da ita gara ta koma gidan ta taga gara ta kyaleta, tana cikin walwala da farin ciki a gaban nasu, kamar bacin ranta shine ace ta koma gidan Habibu Nahuche.

Ita kuma haka kawai yaron ya shiga ranta, yana da wata irin *Charisma* da ba duka maza Allah ya mallakawa ba. Zuwan sa biyu gaida Daddy suna haduwa da Yafendon a falon saukar bakin Daddy, tayi ta zolayar sa wai biko yake zuwa a inda ba'a son sa. Shikuma baya shiru ramawa yake yi, yace yanada kamar ta me zai yi da wata Rahinah? Shi Yafendo ta ishe shi rayuwar duniya. Ya zo ne ya ji lafiyar dan sa a wurin

Daddy he's not here for RAHINAH!

Bata jima da dawowa daga dakin Yafendo ba ta ga wayar ta na haske, alamar shigowar sako text. Ta dauka ta duba sai taga cewa alert ne na kudi Euros €3000. Daga Habibu Aminu Nahuche. Ya cika alkawari na farko da Daddy yasa shi ya dauka na ciyar da ita har sai ta haihu.

Bata san ya aka yi ya aka yi ba kawai ta ji kwalla ta cika idanun ta.

****

Rayuwa ta cigaba da gudana yadda suka tsara ta, sai dai kuma sau tari ta kan zo wa dan adam da sauye-sauye; abin nufi, cikin ta na girma ra'ayin ta na canzawa akan sa. From negative to positive. A kullum

ta ji shi yana wutsilniya sai ta ji gabanta ya fadi, sannan kauna irin ta UWA ta soma kanannade ta ba tareda ta yi shawara da ita ba. Bata son uban cikin, amma tana jin zata iya yin komai don tsira da wannan dan na cikin ta. Shi kadai ne ya rage wanda zata kalla ta kira jinin ta, tunda har gobe bata da wanda zata kira nata a gefen ta.

Ta yi sallama a dakin Yafendo, ta sameta tana murza goge a magogi tana hambudawa, Yafendo tace "yau tun safe ban ji motsin ki ba, inji dai lafiya kuka tashi?" Ta zauna gefen Yafendon, tace "lafiya na tashi Yafendo ina wani group discussion ne da 'yan class din mu via zoom. Sai yanzu muka gama kuma dole yau zan shiga makaranta akwai littafan da

zan karbo a library". Yafendo tace "a wannan yanayin da kike 'yar nan? Zaki niki hanya ki bar gari zuwa makarantar nan taku mai nisa?" Tayi murmushi ta dora hannunta akan na Yafendo tace "kada ki damu tawan, ina jin karfin jikina sosai, kuma direba zan kira mu tafi tare". Yafendo tace "in kin ga wannan naman da ake cusawa cikin fulawa ki sayo min, irin wanda kika kawo min wancan zuwan naki makaranta" tayi dariya tace "bakin Yafendon mu akwai son cin dadi, zan kawo miki shawarma, nima yau ita nake son ci". Da haka suka yi sallama ta daga wayar ta ta kira Yohana direba.

Suna tafe akan titi tana nazarin wani practical da zasu yi cikin ipad dinta, tayi shigarta

islamically **cikin abaya ruwan makuba da mayafinta kirar kasar Oman, cikin ta ya fito sosai yayi toro don ta shiga wata na bakwai. Sake-sake take a ranta ko yaya haihuwa take?** ***Is it painful?*** **Shikuma raino da** ***breast feeding*** **ya suke? Kamar amsa ga tambayarta dan cikin ta yayi wani uban juyi da yasa saida tasa hannu ta dafe shi, tana mai addu'ar Allah ya raba su lafiya.**

Ta nunawa Yohana inda zai ajiyeta, wato ***parking lot*** **na Cologne Public Library. Ta bude kofa ta fito a hankali tana taku irin na masu ciki, ta shiga library din da kafar dama domin kuwa shima shigowar sa kenan. Kamar kullum yana cikin kayan sa na hausawan usul jamfa da wando na farin**

boyel, amma yau bai sa hula ba, ya tara suma mai yawa akansa ta yadda farin gilashin da ya sanya ya nitse cikin gashin kansa. Yana zaune a kujerar sa cikin wani dan cabin na glass inda yake kula da bangaren ajiyar littafai masu muhimmanci (reserve section) ya ga wucewar ta amma ita bata lura da shi ba, kuma gabadaya ta manta a wajen da yake aiki kenan.

Taje ta zabo littatafan da take bukata, amma bata samu guda biyu ba an ce suna *reserve section.*

Ta tako a hankali zuwa *reserve* din, ya juya baya yana fuskantar allon kwamfutar dake gaban sa, kwarai ya ga sanda ta taho, kuma ta taho ne tare da bugun zuciyar sa. Ta

kara wani itin kyau da sulbin fata tabbacin tana cikin kwanciyar hankali, sabanin shi da rayuwar sa ta jirkice bakidaya tun shigowar ta cikin ta. Rahinah muguwa ce mai son kanta da la'akari da maslahar kanta kadai. Idan wani barin na zuciyar sa ya so kare ta, wani baya mata uzuri cewa yake bata da hujjar kin koma maka..... tunda ka ce zaka canza zuwa yadda take so.

Babu wani bangare na zuciyar sa dake yarda wai Rahinah bata son sa.....tana amfani da kalmar ne don biyan bukatar kanta.

"Hi, can you please check these for me?";

-Diagnosis in Otorhinolaryngology

-New Aspects of Fundamental Problems of Laryngology and Otology

Pediatric Otorhinolaryngology....Scott-Brown's Otorhino....." sauran maganar ta makale gabadaya a makoshin ta sakamakon juyowar sa gabadaya. Saura kadan numfashin ta ya bar gangar jikin ta sabida wani mummunan kallo da Habib ya jefa mata. Dadi da cewa bata tsammaci ganin sa ba a daidai wannan lokacin. Sannan dadewar da ta yi bata ganshi ba ya dada haifar mata da faduwar gaban. Tayi kokarin maida numfashinta amma ya gagara isa huhunta.

Daga sanda ya taso daga mazaunin sa zuwa isowar sa gabanta Rahina bata farfado

daga suman tsayen data yi ba. Haka kama hannun ta da yayi suka bar cikin library din bata iya ta kwaci kanta ba. Saboda gabadaya bakin ta ya mutu ta kasa saita kanta a gabansa, ta kasa kuma yin kowacce irin hobbasa ta kwace hannun ta daga cikin nasa.

A sanin ta da shi dai bashi da mota, amma ya bude bayan wata mota opel-astra ya sanya ta ciki ya rufe harda mukulli. Ya zagaya ta barin mazaunin sa ya zauna kuma ya tashi motar da wani irin mahaukacin gudu, bata raba daya biyun yau tata ta kare. Don ta san Habibu akan ta wani mahaukaci-mahaukaci yake komawa.

Har kofar flat dinsa ya shiga da motar, ya kashe ta sannan ya dube ta da idanun da

suka kada, suka kuma sanya hantar cikinta kadawa. "Ki fita mu je, magana kawai zamu yi in mayar dake inda na dauko ki".

Rahinah ta soma hawaye, tace "babu inda zani, nida shiga wannan gudan sai dai akai gawata""ko? Zaki shiga ne kuma da ran ki da lafiyar ki, ko ta tsiya ko ta arziki, kina sane da cewa har yanzu matsayin matata kike?"

Wani karfin zuciya ne ya zo mata, ta ce "wallahi ko ka bude min na fita, ko nayi maka ihun da zaka fada hannun hukuma, nace bana yi, bana so kuma bana auren dole ne?"

Ya kwantar da kai akan sitiyari yana kallon ta, masifa take yi tun karfin ta amma zakin muryarta kamar busar sarewa yake jin sa a kunnuwan

sa. Haka mace mai cikin take komawa? Danya sharaf? Komai fresh? Idanuwan sa har wani kanakancewa suka yi suna dubanta da siga mai nuna bukatuwar miji zuwa ga matar sa……

"You can scream…. (kina iya yin ihun) amma ki sani nima inada nawa 'yancin da musulunci ya bani, kuma zan tabbatar miki shi yanzu". Ya karasa maganr ta hanyar kamota da karfin gaske ya rungume ta, tana mutsu-mutsun kwatar kanta. Yace "Rahinah ki dubi Allah ki tausaya mun……my life is shattered without you. Ko me kike so zan miki, ko me kike so zan zama. Nayi alkawarin fin Romeo iya soyayya. One more last chance…. ko don albarkar

dana dake karkashin marar ki. Rahinah ko a lahira wani kan ci albarkacin wani. In kika barni gabadaya bazan iya kara aure ba. Zan yi ta zama da dan ki ne yana debe min kewar ki har karshen rayuwata……".

Rahinah ta ga cewa hargagin ta ko cika bakin ta bai kwatar ta hannun Habibu a yau, he's ready to face anything don ganin ya kusance ta a yau, wanda hakan na nufin maida hannun agogo baya. Tun farko ita wane tsautsayi ya kawo ta library bayan ta san anan yake? Ta soma kuka tana rokon sa "don Allah ka amida ni inda ka dauko ni, kaga bani da lafiya, bazan iya wannan abun ba zan mutu, da na ma zai mutu, wallahi nayi alkawarin zan saurareka da duk abinda ka zo

da shi amma bayan na haihu....". Habib ya sassauta rikon da yayi mata, shima bazai so wani abu ya samu dan sa ba, dan da yake jin duk duniya ba abinda yake so kamar sa in ka dauke Haj. Kaltume.

"Kin yi alkawari zaki saurare ni in kin haihu?"

Ya tambaya *in a subdued voice.*

Da sauri ta gyada kai, ba don ta yarda ta yi alkawarin a karkashin zuciyarta ba, fatan ta ta rabu da Habib lafiya ba tareda ya maida ita gidan nan nasa ba, data yi alkawarin ita da shi sai dai a kawo gawar ta.

Sai jin Habibu tayi yana dauke hawayen fuskarta da halshen sa, wani al'amari tamkar *electrical shocking* ya bakunce ta. Ashe ba a iya nan

zai tsaya ba? Al'amarin da ya biyo baya mai tsauri da nauyi ne da ya shallake tunanin ta. He began to kiss her passionately wani abu da bai taba faruwa tsakanin su ba. Ko ya manta a inda suke, ko kuma ita ta manta cewa sakakkiya ce a wurin sa. Wani incident da ya dauki tsayin mintuna masu yawa da bazai taba gogewa daga kwakwalwar Rahinah Omar ba. Ya kuma goge tabon abubuwa masu yawa da suka samu muhalli tuntuni akan Habibu Nahuche a zuciyar ta.....

Wayarta ce ta dauki tsuwwa....kira ake akai-akai. Da sauri ta ja baya.... tana wani irin hararar sa tamkar idanun ta sa fado kasa. Habibu ya

shafa kai, yana kallon ta da dukkan kauna da soyayya na zuciyar sa, idanun sa har shigewa ciki suke sabida azabar soyayya. Shi kadai ya san azabar da yake dandana. Komai ya dawo masa sabo, ji yake tamkar bai taba kusantar Rahinah ba sai a wannan lokacin. Amma ya san ko shi maye ne Rahinah bazata sake bashi wannan damar ba, idan har ba ya ya yi yaqin kwatowa kansa soyayya ba.

"Nene!"

Sunan da ya bayyana akan screen din kenan. Gabanta yayi wani irin faduwa. Me ta aikata? Me take aikatawa rayuwar ta? Dadin bakin namiji ne zai sa ta gurbata kyakkyawan ginin data faro? Ya su Nene zasu ji in suka ji tana tare da Habib ne a kofar

gidan sa cikin motar sa ba tasu ba? Bayan ba yadda basu yi da ita ba kan ta koma masa amma tace a'ah? Me yasa ta yarda ta biyo shi? Shin idan Nene ko Ambasada suka san tana tareda Habibu ba zasu zargeta da raina musu hankali ba?

Da wani irin zafin nama ta bude murfin motar ta fice, Allah ya so ta ya saki lock din, ta leko ta window tace cikin muryar kuka.

"Allah ya isa taba ni da kayi, Allah ya saka min!".

Habib Nahuce. Bai san sanda dariya ta kwace masa ba duk da halin da yake ciki. Yace "Allah ya saka mana tare Rahinatu! Akwai mugu a duniya irin ki? Kin ci albarkacin Baby na, na rantse da sai kin kunshi wani sabon cikin a yau kin

haifo su tare sun zama biyu.....". Bata tsaya sauraron mugayen kalamansa ba masu kama da sabon Allah a kunnuwan ta ta nufi titi da mugun sauri tana tare taxi.

Yohana sai ganin ta yayi taxi ta sauketa a gefen sa, ita da tace library zata shiga ta karbo littafi ta fito. In ya kirga daidai ta kwashe akwalla awanni biyu kenan. Ba wannan ne ya bashi mamaki ba sai yadda ta bude motar ta afko kamar wadda aka biyo.

"Are you okey Madame?"

Ya tambaya calmly.

"I'm okey Yohana let's go, kada ka tsaya a ko'ina sai mun isa Frankfurt".

"Is someone following us? So that i report to police?"

"A'a babu mai bin mu, kaidai ka tafi da sauri ka bar harabar wajen nan".

Ya ja motar suka bar wajen yana cewa "alright Madame, but kowanne karamin abu ki dinga gaggawar sanar da police".

Ita dai tace masa ta ji.

Sun yi nisa sosai wayar ta ta sake kara, tayi ajiyar zuciya sai yanzu ta fara samun nutsuwa data tabbatar sun fita daga shiyyar birnin Cologne. Sun kama hanyar da zata kai su Frankfurt.

Da ta duba sai ta ga 10 missed calls daga Nene.

A take ta kira ta jikin ta har rawa yake, ji take kamar Nene ta ga komai da ya faru, ita da Habibu a mota suna kissing. Wani hawayen bakin ciki ya

zubo mata, ta ji ta tsani kan ta, ta tsani karatun da ya fiddo ta daga gidan Ambasada, in bata yi wasa ba Habibu na gab da sake rusa mata rayuwa.

"Nene wallahi ina cikin library ne wayar kuma na barta a mota"

"Meyasa kika je makaranta baki jira ni na dawo mun je tare ba idan zuwan ya zama dole? Kinsan Dr. Yace ki daina zirga-zirga" ta share wani uban gumi daga kan goshin ta, tace "Nene i'm sorry littafai na je amsow na clinical assignment dina, kinga ma ban samo su ba, bazan ma kara zuwa ba har sai na haihu. Zan gayawa Daddy a nemomin na saya kawai" Nane tace "better, me zan dafa miki kan ki iso?" Tayi murmushin samun relief tace "anything

traditional""to shikenan zan miki tuwon alabo miyar ugu leaf da alayyahu da ganda da busashshen kifi, yayi miki?"

Wani hawaye ya bullo mata, ashe haka soyayyar UWA ke da dadi? Allah ya barta da danta itama ta bashi kauna irin wannan. Allah yasa kuma kada mutuwa ta raba su yana karami sai ya mallaki hankalin kansa ko da zata mutu. Ya zamo cewa ta gama bashi duk wata kulawa da tarbiyyar da ya kamata ya samu daga gareta.

A wannan daren, daga Habibu Nahuche har Rahina Omar, babu wanda ya iya ya runtsa. Dare ne mai matsanancin hazo, cikin watan Nuwamba, Habibu na nannade cikin bargo sanyin kasar Jamus na shigar sa, ba abinda yake so

yake bukata a lokacin sai dumin matar sa Rahinah. Amma ta wace hanya zai bi ya dawo da damar da ya samu a baya? Masu iya magana dama sun ce opportunity comes only once in life! Ya bata komai, ya dade da bata komai, ya riga ya bata rawar sa da tsalle. Haduwar su a yau ta maida masa komai sabo *in itsown special unique way*..... girman Rahinah da soyayyar ta sun karu sun ninku sun hauhawa a zuciyar sa, ya fahimci abubuwa da dama wadanda a baya bai sani ba; Rahinah na daga cikin kasaitattun mata da samun kamar su sai an tona. Irin matan nan ne *one in million* wadanda duk namijin da Allah yayiwa baiwar mallakar su ya gama bashi rabin addini sa, ya

gama bashi farin cikin rayuwa, da duk wani jin dadi dake cikin ta.

A yau ya amince da abinda a baya ya ki *believing* da gangan. Cewa zai iya rayuwa babu Rahinah, zai iya hakuri da rayuwar sa *single* ba tare da Rahinah cikin ta ba. A yau ya yarda ya amince rayuwar sa bazata taba zama straight ba ba tareda Rahinah a gefen sa ba. Ko zata yarda ta saurareshi idan ta haihun kamar yadda ta yi alkawari? Shi kuma zai yi komai don dawo da ita cikin rayuwar sa cikin martaba da mutuntawa, dadin dadawa soyayya mara yankewa har fiye da wadda bata tsammani. Daga wannan ranar yake bincike, wani irin bincike na yadda ake tafiyar da soyayyar mata. A

rubuce-rubuce na masana ilmin psychology (self-help books and self-reflection). Ya samo wasu tips guda goma wadanda suka ce (How to keep your woman and make her love you forever). Marubucin ya ce; cikin abubuwanda zasu rike maka soyayyar matar ka sun hada da;

-work on yourself ; ka yiwa kanka self-evaluation; ka cancanci ta so ka ko a'ah?

-listen to her (and i mean really-really listen); ka saurareta akan duk abinda ta zo da shi da cikakken attention ka bata hankalin ka a lokacin da take bukatar hakan.

-learn how she prefers to be loved; ka duba abinda tafi so ka nuna mata soyayyar ka da shi.

-give her gifts (ka kasance mai yawan yi mata kyauta, kyauta tana kara dankon kauna).

-be honest with her (ka zamo mai gaskiya da kyakkyawar manufa akan ta).

-respect her (ka girmamata) and treat her with this respect.

-find creative ways to tell her that you love her (ka zama mai iya kirkirar hanyoyin gaya mata yadda kake son ta in your own special way).

-allow yourself to be vulnerable; wato ka dinga nuna mata raunin ka. (Allow yourself to make mistakes and admit to them. Allow yourself to be real and true and not hide any of yourself from her.

Don't be afraid to cry in front of her. And don't be afraid to let her cry, too. Vulnerability allows for deep connection and bonding in a relationship. If you can't be yourselves in your most raw forms, how are you supposed to feel safe building a whole life together?"

Habeeb Nahuche sai ya ga cewa duka wadannan *tips* din da wannan masanin ya zano duk zurfin ilmin sa shi bai mallaki ko daya ba! Bai taba nuna wa Rahinah dayan su ba, *yet* yana *blaming* din ta da kasa son shi duk cancantar sa.

Ita soyayya ta gaskiya ba ta ta'allaka da *appearance* din mutum, but *the way he demonstrates himself.*

Ya yarda duk ilmin ka ilmi baya taba karewa a duniya, saidai ka dauki iya wanda zaka iya ka bar ragowar.

Inama! Inama! Inama Rahinah ta yarda ta sake bashi dama koda sau daya ne a rayuwar su???

****

A nata bangaren, Rahinah Omar, kwana tayi tunanin abinda ya faru a yau, tana mai tariyo komai dalla-dalla. Idan zuciyar jin tausayi ta kutso, sai zuciyar neman kwatar 'yanci ta hambare ta. Mutumin da bai ji tausayinta ba, ita akan me zata ji tausayin sa? Yana son ta koma ne don bukatun kansa amma bai taba tunanin ya tambayeta asalin ta ko na iyayen ta ba. Wanda ke kara tabbatar da cewa ba damuwar

sa bace personal life din ta, abinda yake yimawa kawai shine a gaban sa.

Ita wannan soyayya ta Habibu ta kasa ganeta, domin ta hada biyu da uku bata bata ma'ana ba. Tana burin auren mijin da ke matukar son ta, wanda zai rungumi maraicin ta kada yayi amfani da shi ya cutar da ita, wanda zai so ta da dukkan zuciyar sa. Amma Habibu fa? Ta tabbata ba don cikin nan ba da daga ranar da ya sake ta bazai kara waiwayota ba tunda duk abinda yake so daga gareta ya riga ya same shi.

Tsaki tayi ta juya a hankali don taji dadin kwanciyar ta, sai taji gefen wuyan ta na kamshin Carolina Herrera (men) har zuwa lokacin. Abinda ya tuna

mata da *incidence* din. Is what happened Haraam? Bata sani ba, in haramun ne tana neman gafarar Allah, domin kuwa bata da laifi, laifin ta shine kasa yi masa gardama wajen binsa tamkar rakumi da akala. "Ya salamu sallim". Ta fada a fili. Amma wani sako na zuciyar ta na gaya mata *it's not haram* din, tunda har yanzu cikin iddah take. Kuma abinda addini ke so a wannan tsakanin shine su yi sulhu. Sulhun da bata jin har abada zata yarda da shi.

Washegari Nene ta rakata anti-natal da suke zuwa duk sati, likita ta dubata sosai ta kuma ce baby is breach sai an gyara masa kwanciya. Haka ta daure aka gyara sannan ta karasa duba ta, tace tanaso tayi mata alfarmar zuwa dakin

haihuwa tare da mijin ta, sabida suna so mata su dinga haihuwa akan idanun mazajen su, domin neman karin kauna da soyayya, jin kai da tausayi a garesu. Gashi bata taba ganin ta ta zo tare da shi ba.

Rahina dai bata ce komai ba, sai Nene ce ta ce baya kasar ne, amma in ya dawo kafin ta haihu da shi za'a shigo labour room.

Rahinah ta daga 'yan idanun ta taba kallon Nene kamar tace da ita akan me za ki mata karya! Mun rabu, short and simple. Sai ta tuna abinda Ambasada ya taba gaya musu cewa saki ba karamin abu bane a kasar jamus, and it should be abiding by German law. Don haka rufe zancen da Nene tayi kawai shine daidai.

Watanni biyu a gaba, ta shiga watan haihuwa, ta kuma gama shekarar farko ta karatun ta. Wato tsayin semester biyu. A haka take zuwa zana jarrabawa da tsohon ciki har ta kammala da kyakkyawan sakamako. Ambasada ya baiwa Nene kudi yace ta saya mata duk abinda zata bukata na haihuwa ba ruwansa da abinda Habibu zai bayar.

A daren ranar ne kuma sai ga tarin akwatuna shaqe da sitturun jarirai unisex daga Habibu Nahuche. Hatta pampas da feeding bottle sai da ya sayawa dan sa, amma ita ko tsinke bai saka da sunan ta ba. Wannan ya sosa mata rai ba don tana son abin hannun sa ba, a'a yadda ya nuna yafi son

abinda zata haifa yanzu akan ta shine abinda ya sosa zuciyar ta.

"To a kan me?"

Zuciyar ta tambaya.

"A kan dalilin da nima ban sani ba!" Ta amsawa kanta a fili.

****

EDD dinta saura kwana biyar rannan da daddare suna zaune a dakin Yafendo suna cin tuwo taji damshi-damshi daga kasan jikin ta. Bata kawo komai ba sabida sabida bata ji ciwon komai ba. An ce mata kuma ciwo ake ji mai tsanani.

Amma ba'a dauki wani dogon lokaci ba ta soma 'yan mutsu-mutsun da ya ja hankalin Yafendo kanta.

"Yar nan lafiya kike yanka gumi haka?" Tayi yake tace "bakomai fa Yafendo, zafi kawai

nake ji" Yafendo ta gyada kai ba don ta harda ba suka cigaba da hira. Safeenah ta shigo ta gaida Yakumbo, sannan ta dubi Rahinah tace "Nene ta ce kina da bako a falon Daddy……." amma kafin ta kai karshen maganar ta sai gani suka yi tana shure-shure. Yafendo tace "Aha! Ni na san abun ne ya zo, kika yi mirsisi ke ga jaruma. Ke Safeentu kira Nenen ku ki gaya mata haihuwa ta zo a kawomin reza". Safeenah ta zaro ido sannan ta fita a guje, kada taje ayi haihuwar a gabanta.

Nene ta fado dakin da gudunta, tace "Yafendo wace irin Reza? Ki rufa min asiri in mutu maza su kai ni, ba'a kasar mu muke ba inda ake haihuwar gida. Maza kwarara jikin ki Rahinah mu gangara asibiti, ga

Habib nan yana nan ya zo sai ya kaimu tunda direba bai dawo ba har yanzu."

Tsananin halin da take ciki, shi ya hanata yin musun tafiya asibiti tare da Habibu kuma a cikin motarsa. Daga ita sai Nene a baya tana shafa mata kanta da bayan ta tana yi mata addu'a yayin da shi yake tuki cikin wani mawuyacin hali. Ji yake da zai iya da ya karba mata nakudar, kanar yadda ya zamo silar wahalar ta daga zuwa karatu.

Sun samu ganin Dr. Saliha Widad wato likitar data ke gani itace on duty, nan da nan ta karbeta akan gadon tura marasa lafiya daga hannun Habibu da ya sunkotota gabadaya daga cikin mota zuwa cikin reception. Dr. Saliha ta

duba ta tabbatar haihuwa ce gadan-gadan sai ta fito tana kiran sa. Ta tambayi Nene shine mijin Rahinah? Nene ta gyada kai ba tareda ta ce komai ba, yayin da likitar tace "kazo ka tsaya tare da ita, ka ga yadda dan ka/'yar ka zai iso duniya".

Habibu ya hada kai da bango yana ce mata "a'ah..." tayi murmushi tace "ashe raggo ne baban baby, Rahinah ta fika juriya. C'mmon ka biyo ni nace". Ya juya yana kallon Nene sai ta gyada mai kai, don bata so a tsaya ana tone-tone. Ai har yanzu tana cikin zummar auren sa.

Tamkar wanda kwai ya fashewa a ciki, haka ya daga kafa ya bi bayan Saliha Widad.

****

"Dada!"

Kawai take kira hadi da sunan Allah,ta yi gumi kashirban, kanta na bisa cinyoyin Habibu gashin kanta ya bazu jikin sa. Ya rike hannayen ta cikin nasa, ita take nakudar amma ya fi ta hada gumi, jikin sa har kyarma yake. Dr. Saliha na fadi tayi nishi baby ya kusan isowa. Da ta daddage ta saki nishin kuwa sai gashi ya fado tare da mabiyar sa. Ya kuma canyara kuka a hannun Dr. Saliha wadda bakin ta ya kasa rufo, shekarar ta kusan goma tana karbar haihuwa amma bata taba ganin haihuwar katon baby black beauty irin na Rahinah ba. Saidai bai dauko komai nata ba

har duhun fatar sa na mahaifin sa ne.

Aka gyarata, aka gyara wajen haihuwar, aka dau baby ana gogewa da man zaitoon aka shirya shi tsaf cikin kayan sanyi, aka nannadeshi a shawul sannan aka kawo mata shi saitin kanta. Sai a lokacin ta soma dawowa hayyacin ta ta kuma ji kamar a jikin mutum take kwance. Tana so ta kalli fuskar babyn amma tana son ganin wanda ya baje mata jiki ta kanannade akai ta haihu haka. A hankali ta daga kanta, sai idanun ta cikin na Habibu, wanda hakan ya haifar mata da matsananciyar faduwar gaba. Kafin ta soma yunkurin tashi ta kuma fashe da kuka.

"Amma Dr. Widad kin cuce ni....." ta fada cikin kuka sosai,

kamar Dr. Na jin harshen nata, tayi Allah ya isa da fillanci, tayi da hausa, tayi da German, tayi davduk yaren data iya. Duk akan Dr. Widad data shigo mata da Habibu dakin haihuwa. Nene tana ta bata baki kan ta yi hakuri. Shikuwa ya harde hannuwa a kirji yana kallon ta da wani irin murmushin SO. In da a ce zai iya, zai iya ciro zuciyar dake kirjin sa ya bata a halin yanzu don kawai ya nuna mata dimbin godiyar sa da soyayyar sa gareta. Bisa bashi farin cikin da wani a duniya bai taba bashi ba. Bisa maida shi UBA, bisa bashi precious gem din da kudi ko mulki basu isa su bawa dan adam ba.

Dr. Ta mika mata Babyn bayan ta gama kukan bakin ciki ta share hawayen ta, da sauri ta

karbe shi tana kallo. Ba shiri ta daga ido ta dubi Habibu. Yaro kamar Ubansa yayi khaki ya tofar. Ya lumshe mata lumsassun idanun sa ya kuma daga mata girar sa daya, "eh dani yake kama ba da ke ba, kamar ya san ba kya son uban sa". Ta gatsina baki ta cigaba da kallon babyn tana tazbihi a zuciyar ta. Wata irin kauna ta da da mahaifi na keta ruhin ta da zuciyar ta. Her only relative, her only blood! Ta yaya bazata so shi sama da komai a duniya ba?

Bata yi aune ba ta ji Habib ya kashe su da hoto da camerar wayar sa.

Hararar sa tayi, duk wani abu da zai bakan ta mata ya san shi, yanzun ma Nene na bada baya ya matso gabanta, "wai

sabida kin haihu gabana kike wannan kukan? Yo wane dare ne jemage bai gani ba? Bani Da na nan in ji dumin sa, kin wani kama shi kin kankame kamar ke kadai kika yi nakudarsa". Ya mika hannu, ta yi maza ta janye dan ta.

"Ba zaka dauke shi ba!"

Ya saki baki yana kallon ta da mamaki, Nene ta shigo jin sautun kukan ta, tace "lafiya? Ki bashi yaron mana ya yi masa khutbah?""Nene bazan bashi ba, da na ne nikadai, ba ruwan shi da mu ba ruwan mu da shi" Nene tace "Rahinah kin san abinda kike fada kuwa? Mahaifin sa ne fa? Yau na ji karfin hali wai barawo da sallama. Ki bashi yaron nan kafin raina ya baci akan hakan". Rahinah ta saka kuka

sannan ta mika masa yaron. Ya karbeshi da wata irin kulawa tamkar ya maida shi cikin sa. Yayi masa khutbah da sunan da ya zaba masa wato sunan mahaifin Manzo SAW. Ya tauna dabino (ajwa) ya sanya masa a baki, yaron ya hau motsa dan bakin sa gwanin sha'awa, Habib bai san lokacin da wasu irin zafafan hawaye suka zubo masa ba. Ya rungume yaron a kirjin sa. A haka Ambasada ya shigo ya same su. Safinah ta biyo bayan sa dauke da kwandon abinci. Ya yi wa Habib da Rahinah "congratulations" sannan ya karbi yaron yayi masa addu'a.

Washegari aka sallame su. Suka koma gida. Tun daga ranar Habib yake zarya, sayo banza sayo hopi, duk don ya

farantawa Rahinah. Amma ina! Zuciyarta ta riga ta kekashe akan Habibu, babu wani repenting da zai yi ya burge ta.

Babban tashin haankalin sa shine Rahinah ta gama iddah, gashi yayi alkawarin bazai maida ita ba da amincewa da yardarta ba, shima Ambasada bazai taba amincewa ba yayi forcing din ta akan abinda ta nuna ta gama bashi baya.

Tsayin watanni uku tana shayar da Abdallah kasancewar suna cikin hutun summer. Ta saba da yaron sosai, bata barci sai yana kan kirjin ta, har fargabar komawa makaranta take, don ta san dole zai koma haunnun mai raino. Ita kam ba wanda take jin zata iya baiwa dan ta ya rike mata yadda take

ji da abun ta. Ko Habibu bata bari ya dauke shi sai in Ambasada yana gidan yayi mata jan ido. Gabadaya Habibu Nahuche ya gama susucewa, ya fita hayyacin sa don zuwa yanzu ya tabbatar da ya rasa Rahinah.

Lokacin da suka koma hutu Nene tace zata samar mata mai raino, amma Rahinah ta fito fili tace da Nene zata yi deferring karatun ta zuwa shekara ta gaba don ta samu damar kulawa da Abdallah. Da bashi cikakken lokacin ta a lokacin da yafi bukatar hakan.

Nene da Ambasada na jinjina soyayyar Rahinah ga dan ta, amma a zuciyar su suna tausaya mata. Don sun san irin wannan kaunar sai ka samu a karshe iyayen da 'ya'yan basa rayuwa tare. Kaunar tata tayi

yawa kuma *silence* din Habibu na nufin wani abu. Yafi watanni uku bai kara takowa inda suke ba tun wani wulakanci da Rahinah tayi masa, inda tace idan ba ita ce autar mata ba, kuma ba daga kanta an daina haifar mata ba, sannan shi ba maye bane to ya fita hanyar ta ya je ya nemi wani gantalallen auren amma ba nata ba, tun daga ranar bai kara takowa ba, amma sakon shigar kudi basa yankewa a tsakanin su.

A wannan watan da ake ciki ya kammala rubutun proposal din sa, ya karbi shaidar kammala masters din sa, aka yi musu convocation na graduating. A ranar da ya karbi kwalin sa ya hada komai nasa don barin kasar Jamus. In bai yi kuskure ba yau ne Abdallah ya

cika shekara daya da haihuwa kuma yana gudun sa ko'ina. Don daga baya ya kan je ganin sa amma iyakar sa falon saukar bakin Ambasada, a kawo masa yaron suyi soyayyar su ta uba da da, ya bashi sayayyar da ya yo masa, ya tafi ya bar shi yana kukan sai ya bi shi. Sun yi wani irin sabo wanda in zaka ga sanda zasu rabu sai zuciyar ka ta motsa, ka kuma tambayi kan ka shin ita Rahina wace irin zuciya gareta? Anya ma tana da tsokar zuciya a cikin kirjin ta?

A wani zuwa da yayi ganin Abdallah, ba tareda sanin ta ba ya fice da shi a mota, tun safe har yamma, a ranar Rahinah har dan karamin hauka ta yi, Nene na kwantar mata da hankali tana gaya mata bazai ki dawo mata da dan ta ba tunda

nono yake sha. Yafendo kam haushin Rahinah ta koma ji sabida rashin kawaicin ta akan yaron, tace ita bata taba ganin mara kunyar bafullatana irin Rahinah ba, rashin kunyar tata shahararriya ce kuma a kan dan fari, inji Yafendo. Idan ta kaita bango kuma ta ce "kinibabbiya, sanda tasa Uban sa a daki yayi mata cikin sa ai bata ce masa rowar sa zata yi masa ba idan sun haife shi, in da gaske take son yaron ta koma gidan ubansa mana?

Dukkansu basu san inda Habib ya kai Abdallah ya kuma dawo dashi ba.

Rahinah kamar ta shide da Abdallah ya dawo don murna. **

Yayi sallama a falon Ambasada Shehu, shi kuma ya

amsa cikin sakin fuska da mutuntawa kamar yadda suka saba a kowacce haduwar su. Har kasa ya tsugunna ya gaishe shi. Shikuma ya soma yi masa fada akan irin ramar da yake yi, da kyar idan yana cin abinci yadda ya kamata. Ya ce "shi mace bata isa tasa shi a wannan halin ba, don dukkansu daga karkataccen hakarkari aka halicce su. Yana da tabbacin Rahinah zata huce watarana kuma da kanta zata nemeshi ta nemi dawowa dakin ta. Haihuwa a tsakani ba wasa bace. Don haka ya kwantar da hankalin sa.

Habib sai yayi murmushi, his beautiful serene smiles. Ya ce "ai komai ya zo karshe ranka ya dade, na kammala karatuna zamana a kasar Jamus ya kare.

Nazo ne in dauki Abdallah bisa iznin ku, zamu koma gida Zamfara".

Ambasada shiru yayi, hukuncin da yaron ya yanke yayi matukar *impressing* din sa. Da gaske gara yayi nisa da Rahinah ya kuma dauke dan sa, watakila hakan yasa ta yi gaggawar gano muhimmancin su cikin rayuwar ta.

"Amma ka san mai raba ta da dan nan sai Allah ko? Kuma kana da wadda zata kula da shi kamar yadda mahaifiyar sa zata kula da shi? Idan babu, kai namiji bazaka iya rainon da ba, na gaya maka".

"Mahaifiyata tana raye ranka ya dade, sannan Yayata Badiyya, duk cikin su babu wanda bazai rike min shi kamar

koma fiye da yana gaban mahaifiyar sa. Albarkar ku kawai nake bida, da fatan alkhairin ku".

Ambasada couldn't keep his tears wato ya kasa maida hawayen sa. Yayi saurin share su kafin Habibu ya gani. Ya kira Nene ya gaya mata ko me kenan. Itama Nene tafi mijin ta shiga rudun tunanin mai iya raba Rahinah da Abdallah.

Sai ga yaron ya shigo tinkis-tinkis, cikin tafiyar shi mara kwari, ya yi kyau cikin kayan sanyi, yana ganin Babansa ya tafi da gudu ya fada jikin sa. Habib sai ya ga kawai bari yayi amfani da wannan damar, kada dama ta biyu ta sake kubuce masa.

"Zan tafi dashi yanzun nan ranka ya dade, ku gafarce ni"

Nene ta soma kuka, ta saba da yaron ya shiga ranta da zuciyar ta duka. Daga ita har Ambasada aka rasa mai karfin halin hana Habibu wannan danyen aikin, har ya fice falon da yaron a kafadun sa. A lokacin da Rahinah ke dakin ta tayi dai-dai a tsakiyar gadon ta tana ta sharar barci abinta.

"""""

Koda ta farka bata ga yaron ba bata damu ba, ta dauka yana wasan sa ne a dakin su Ahlan kamar yadda ya saba. Tayi wanka ta ci abinci ta koshi ta janyo littafanta ta karkade, gobe ne zata koma makaranta daga deferring din ta. Saboda haka tana bukatar dumama kwakwalwar ta, duk da cewa a son karatu irin na Rahina ko da bata zuwa makaranta kuma

babu jarrabawa a gaban ta bata fasa bitar littafanta ba lokaci-zuwa lokaci.

Amma ga mamakin ta har tayi sallahr maghriba da Isha Abdallah bai shigo ba, bata kuma ji tashin muryar sa ba. Nene kuma tana sassan Daddy a irin wannan lokacin, watakila kuma ya bita can din ne.

Amma da lokacin kwanciyar su yayi bata ganshi ba dole ta fito tana kwala masa kira. Gaban Nene da ke daki ya bada dam! Tayi zamanta a daki ta ki fitowa, sai ga Rahinah ta shigo.

"Nene ashe kina nan? Abdallah nake ta nema tun rana rabo na da shi". Nene ta daga ido ta dubeta idon ta fal tausayi, ta ce "yaki Rahinah, zo nan mu yi magana".

Rahinah ta soma shiga tashin hankali, ta dafe kirjin ta da hannayen ta da karfi, "ba dai wani abu ne ya same shi ba Nene?""Ba abinda ya same shi Rahinah, he's healthy and vibrant, amma Baban sa ya ce mu gaya miki ya zo ya tafi da shi, idan kin canza ra'ayin ki kan zaman ku tare ku raini yaron tare ki fada masa zai dawo ku koma auren ku!"

Rahinah ta dora hannuwa aka ta zuba ihu, sannan ta sulale a wurin babu yadda take, tamkar wata mai tashin jinnu ta koma tana kuka tana birgima a kasa tana kiran Abdallah ".....wayyo da na, wayyo Abdallah!" Nene sai da ta firgita ta kuma yi nadamar gaya mata ta wannan sigar, ita ta fada ne don Rahina ta ce ta

amince zata koma dakin ta su kuma su yi wa Habibu magana ya dawo. Amma a yadda Rahina ta karbi lamarin babu zancen sulhu face Habibu Nahuche yayi mata *kidnapping* Da.

Data gaji da ihu da birgima hawaye ya hade da majina duk jama'ar gidan na kanta har Yafendo, hatta Safeenah da bata son ta yau ta tausaya mata. Nene na bata hakuri tana gaya mata abu ne mai sauki, ta yarda kawai ta koma dakin ta ta raini dan ta a gaban ta amma ina! Tunanin Rahina yayi fintinkau da tunanin kowa. It goes far beyond mere or casual assumption.....ta riga ta sanyawa zuciyarta tsanar Habibu kuma bata jin akwai abinda zai kankare wannan tsanar ban da ikon Allah.

Hanya ta saba babu ko lullubi data faki idon Nene ta shiga sallah, Yafendo ma ta koma daki ta rabu da ita, bata manta nisan dake tsakanin Cologne da Frankfurt ba tafiyar awanni biyu ce kwarara a mota, amma ji take zata iya zuwa a kafa.....

Tafe take a gefen titi tana kuka kamar mahaukaciya. Daidai lokacin da anka rufe kofar jirgin Lufthansa....wanda zai tashi zuwa kasar mu mai dimbin albarka. Ba da jimawa ba ya soma rugugin sa mai gigitarwa kafin ya dauki hanya dodar, ya daidaita sosai, ya cigaba da keta hazo a sararin samaniya.....

Ya tafi tareda duk wani farin cikin RAHINAH OMAR.....Ya kassara ta.... ya

raunata jarumtakar ta. A da tana ganin ita jaruma ce zata iya fuskantar komai don ta kwaci 'yancin ta wajen Habibu Nahuche. Ashe wani 'yancin ba ya kwatuwa ta karfi duk yanda anka so, Habibu bai shigo rayuwar ta don ya fita a sanda take so ba. Ya shigo ne don ya dai-daita (shattering) farin cikin ta ya raba ta da sauran *hope* din da ya saura mata a rayuwa……

"Allah ya isa na…..Allah ya isa tsakanina da kai Habibu! Kuma ko zan mutu ba aure, ko haka zan kare rayuwata *single* bazan koma gidan ka ba…..mugu, magulmaci, maketaci, maha'inci, the rapist".

Ita kadai take tafiya tana hada hanya tana sakin zance

kamar zautacciya. Habibu ya shammace ta, shammatar da da ace idanun ta biyu ko duk kotun duniya zata taru a kanta bazata raba ta da danta ba. Ai addinin ma da ya bashi wannan damar sai idan dan ya fara girman da zai iya kula da kan sa.

"Jahilin banza jahilin hopi, algungumi munafiki, in ba tsoro ba ka dauke shi gabana mana? Ai faduwar gaba asarar namiji ce....." babu wani mummunan suna da bata kira Habibu da shi ba, babu mugun alkaba'in da bata yi masa fata ba. A karshe ta fashe da kuka ta durkushe a inda take, data ga ta dauki hanyar barin Frankfurt kuma tafiya ta ki ci ta ki cinyewa. Hankalin ta ya fara dawowa jikin ta ta tabbata

bazata iya kai kanta ga inda zata riski Habibu ba kuma bata da kudin motar da za ta biya a kaita, haka babu katin bankin ta a tare da ita. Wannan ya tabbatar mata har yanzu tana cikin hankalin ta bakin cikin Nahuche bai haukatata ba.

Zata yi amfani da sauran hankalin da ya rage mata wajen gina rayuwar ta, ta ga cewa bata kamu da ciwon damuwa ba, da wajen ganin cewa bai yi amfani da soyayyar da take wa Dan ta ya karasa cin galaba a kan ta ba, ya kara kassara ta, ta hanyar maida ta kurkukkun auren sa, wanda babu komai a ciki sai biyan bukatar ran sa.

A tunanin ta har abada bata son Habibu, kuma har abadan bazata so shi ba. Abin da bata sani ba SO daban, haka

bacin rai daban. Bacin rai *is mortal and LOVE is inevitable.* Watakila kuma ganin ta da shi na farko abinda ta ji akan sa wani abu ne daban ba so ba, wanda ta dinga fatan in sun zo mutuwa a jirgi...to Allah ya sa ta mutu manne cikin jikin sa.

*****

Mu karasa a book 2. Manne suke da juna.